[1/27, 18:31] Zahra muhd mahmud: *ALLAH GATAN BAWA*

*Bismillahirrahmanirraheem*

*Nagodewa Allah mekomai me kowa daya bani ikon rubata wannan littafi nawa me suna *Allah gatan bawa, ina rokon Allah yasa littafina yasamu karbuwa agurinku masu karatu,innayi kuskure kusanar dani da gaggawa domin in gyara ,dan adam ajizine nagode.*

*Page 1-10*

Azaune take akan dakalin kofar gidansu hannunta dauke da kara tana wasa dashi yayin dasauran yaran makwabtansu suma suke nasu wasan ita kuma tana binsu da ido domin ita Bata da yencin shiga cikinsu tayi wasan yarinyace yar kimanin shekara takwas da haihuwa wacce Allah yajabceta da lalura irinta zubar da miyau sanna kafarta daya dahannunta daya duk ashanye suke intana tafiya tana jefa kafarne yayin da hannun yake makale a kirjinta

wannan lalurarce tasa yara da sauran mutanen garin kyamatarta ko wasa basayi da ita sede tazauna agefe tana kallonsu

*Asalin labarinta*

Ilham bukar shetima shine sunanta na aynihi mahaifinta malam bukar shetima hafaffen garin medugurine acikin garin bama inda fadace fadacen daakeyi ayankinsu yayi sanadiyyar mutuwar iyayensa hakanne yasa yayanke shawara shiga cikin ayarin yan gudun hijira domin yin hijira daga yankinnasu. Bashi kadai bane agurin iyayannasa su biyu ne shida dan uwansa mesuna imamu amma rudin dagarin ke ciki yasa suka bacema juna yayi kukan bakin cikin mutuwar iyayensa da kuma bacewar yayansa Wanda besan awanne hali yakeba shiyasa yarungumi kaddara yayi hijira

Acikin ayarin yan gudun hijirarne yahadu da wata budurwa wacce itama ankashe iyayenta( Bata da kowa )me suna maryam tunda suka hadu yake tausayamata sabida ita macece shiyasa yashiga dawainiya da ita har suka shigo garin kano

bayan ansaukesu asansanin yangudun hijirane washe gari yakirata gefe inda yashawarceta dasuyi aurene zefi kulawa da ita sabani basu da aure Batare da Bata lokaciba ta amince inda dattawan cikin yan gudun hijirar sukadaura musu aure bayan yabata sadaki nera dubu biyar

tundaga lokacin yadukufa gurin kwadago acikin gari har Allah yataimakeshi yakama masu hayar gida me daki biyu acan garin wudil sabida beda halin kamamasu acikin gari  be kaunar zamansu acikin sansanin "yan gudun hijirarne shiyasa yakamamasu haya bayan tarewarsu badadewa Allah ya albarkacesu dasamun karuwa ta cikin suncigaba da kulawa da cikin har zuwa haihuwa inda Allah yasa maryam tahaihu lafiya tasamu "ya mace  yarinyar kyakkyawace ajin farko sabida daga uwa har uban shuwa arabne sede kallo daya zaka mata kafahimci Bata da lafiya maana nakasasshiyace basuyi kasa agwuiwaba suka samata suna inda taci sunanta ilham bayan suna ilham iyayenta sundukufa neman magani amma duk inda sukaje amsa daya akebasu bazata warkeba tunda da lalurar aka haifeta hakan yasa suka hakura suka mikama Allah lamarinsu

ilham na dada girma lalurarta nakara bayyana ahaka har aka yayeta bayan yayetane Allah yasake basu wata 'karuwar inda wannan haihuwarma tasamu mace suka samata sunan mahaifiyar bukar fateema suna kiranta ameera bayan haihuwar ameera basu sake haihuwaba har zuwa yanzu da ilham kede shekara takwas ameera kuma biyar

rayuwa suke mecike da tsanani sabida malam bukar me karamin karfine wani lokacin ko yafita bayasamun dakon haka yake dawowa ahaka yakokarta yasa su ilham awata makarantar gwammanti ta pramary ilham na aji uku ameera aji biyu duk à tunaninsu ilham bazata iya komai amakarantaba amma Allahyataimaka yasa tana ganewa sede ko tambayarta akayi bazata iya fadaba sede gwaranci dan harshenta akarye yake. ko amakaranta tsokanarta suke yara sede ameera tatunda taremata dukda itama bawani wayo garetaba ita ilham kuwa sede taita dariya miyau nazuba tadauka wasa suke mata, to ko sundawo gidama yaran unguwa bakyaleta sukeba shiyasa mahaifiyarsu batason ilham nafitowa sabida ko ina hantararta akeyi tun mamansu na magana har tadena sabida tasan *Allah gatan bawane*

*Cigaban labari*

tanana zaune yaran suka fara tsokanarta itako se dariya take harda kwantawa miyau nazubowa daga bakinta, jiyo hayaniya da mahaifiyarta tayine akofar gida yasa tayi saurin lekawa daki inda tabarsu suna wasa da ameera ga mamakinta ba ilham sede ameera datakeyin homeworke dinta dasauri tadauki hijab dinta tasa tayi kofar gida sabida ta tambatar da ilham akeyi ayko ilai tana fita tayi tozali da ita

tana dariya yara natsokanarta suna watsamata kasa bakinciki besa tayi yunkurin hanasuba illa iyaka dauko ilham datayi tashiga gida daita itako baabinda yadameta se dariya take .

love you all maman yusuf□□□□□□□□□□

[1/27, 18:31] Zahra muhd mahmud□: *ALLAH GATAN BAWA*□□□□□□□□□□

_Writting by Zahra Muhammad mahmud_

*Page 11-20*

Suna shiga gida kai tsaye  toilet tashige daita tsifa tafara yimata sannan tawankemata kai Wanda yasha kasa sannan tayimata wanka tafito daita daki takaita sannan tayimata shafa tasauyamata kaya karkuso kuganta à time din kamar kadauka kagudu sabida kyan datayi.

Abinci tazubo mata tafara Bata abaki Wanda ita ilham har zuwa lokacin dariya takeyi sabida intafara dariya tana jimawa bata denaba itako mahaifiyarta kwalla kawai take sharewa natausayin diyar tata

**********

Yauma kamar kullum suntaso daga makaranta, ameera narike da hannun ilham suna tafiya yara suna tsokanarta ameera sekuka take musu tana dan Allah kudena metayimuku Wanda agefe daya ita wacce abin yashafa inbanda dariya baabinda takeyi ganin hakane yasa yaran suka cigaba da tsokanarta ahaka har suka karaso gida babansu suka tarar akofar gida yana alwala  zashi masallaci ganinshine yasa yaran komawa da gudu sabanin da dahar cikin gida suke binsu

Sannu baba mundawo cewar ameera sannunku mamana kushiga gida ina zuwa bari nayo sallah yafadi tareda shafa kan ilham wacce takafeshi da ido ba um ba umum

Dashigarsu gida dakin mamansu suka shiga suka tarar da ita ta kabbara sallah ameerace tayi kokarin zuwa daukar buta itama tayo alwalar tazo tabi bayan mamanta sukayi sallah. Tare da yima ilham adduar samun sauki.itako ilham kiciniyar cire safa take har suka idar bata cire KO guda dayaba ameerace taamsa tacire mata sannan mamansu tacire musu Uniform Wanda gaban rigar ilham jike yake da miyau Wanda hakanne yatilastawa rigar kodewa daga gaban  wanka tamusu sannan tajika musu garin rogo suka sha

bayan sungama sha ne malam bukar yashigo gida fuskarsa ba walwala kan tabarmar dasuke zaune yazauna cike da kulawa maryam take tabayarsa malam meke faruwa naga ranka abace. Yace haba maryam dama haka yara suke biyo ilham baki taba sanar daniba kamar sunga dodo Sun m'aida ita kamar abin wasa haba maryam kinyimin adalci kenan. Maryam wacce tunda yafara magana take zubar da hawaye dakyar tabudi baki cikin kuka tace haba baban ilham menene amfanin insanar dakai indaga hankalinka yarannan badenawa zasuyiba konakai kara gun iyayensu basa kwabarsu to yazanyi ilham de ba ita  tayi kantaba Allah ne yayi ta kuma shi dayayita ahaka nasan yanasane daita kuma nayi imani shine gatanta danhaka kaima kazubama sarautar Allah ido inda rabon musha kallo nangaba zakace nafadamaka takarasa zancan tana kuka. Jin maganganunta yasanya jikin bukar sanyi cikin sigar rarrashi yafara magana nafahimceki maryam kuma nima zanyi yadda kikace amma kinsa ba dadi adunga tsokanarta tace hakane amma bamuda yadda zamuyi sede mufadawa Wanda yayita

haka sukai ta tatyaunawa agame da matsalar ilham har akakira sallar laasar suka tashi domin bada fatali.

love you all 😘 maman yusuf

[1/27, 18:31] Zahra muhd mahmud□: *ALLAH GATAN BAWA*□□□□□□□□□□

_writting by Zahra Muhammad mahmud_

*Page 21*

*Bayan shekara uku*

Kwanci tashi bawuya agurin Allah yaune ranar dasu ilham suka gama pramary school ita da ameera sabida tun suna aji hudu akayima ameera jumping takamo ilham.cike suke da murna daganin ranar dagasu har iyayensu murna suke harda ilham wacce batasan meyakawo murnarba.atamfa 'yar leda babansu yasiyamusu akadinkamusu Riga da siket ba laifi sunyi kyau kuma sunji dadin kyautar da babannasu yamusu na atamfar,

*********

Yau watansu ilham daya dagama makaranta suna zaune atsakar gidansu suna wasa yayin da iyayensu suke hirar rayuwar duniya. Yarone yashigo gidan da sallamarsa bayan Sun ansa yagaishesu sannan yadubi malam bukar yace baban ilham ana sallama Dakai akofar gida wani mutumi gabanshine yafadi sannan yace kaje kace ganinan zuwa yaron yamike yafita yayin da malam bukar shima yamike, da sauri maryam tasha gabanshi tace "abban ilham yanaga daga cewa ana sallama dakai hankalinka yatashi kode akwai matsalane. Hannu yasa yashare gumin daya keto masa yace "Maryam banfada mikibane amma wallahi tun watanni uku dasuka wuce kudin hayarmu yakare kuma megidan cemin yayi yabani wata biyu inkawo masa kudin inba hakaba zesa wasu agidan kuma kinga yanzu har wata uku shida yacemin wata biyu nasan yazo karbar gidansane shiyasa kikaga hankalina yatashi. Cike da damuwa take kallon mijinnata tace "meyasa bakason sanar dani damuwarka abban ilham ni aganina abokin kuka shi ake fadawa mutuwa  meyasa kaboyemin ?  Kiyi hakuri itace kalmar daya iya furtawa yafita kofar gida dan ganin me sallama dashi abinda yaguda shiyatarar megidan yagani atsaye dashi dawasu katti guda biyu  tun kafin yayi magana megidan yarigashi yafara magana cikin fushi "sannunka mallakau wannan ay ko gadona gareka se haka ko ancemaka abanza nasamu gidan dazan barka kaita zama batare dakabiyaniba cikin muryar tausayi malam keba megidan hakuri har kasa yaduka yana bashi hakuri amma shi KO ajikinshi karshema wainnan katti yacema sushiga gidan sufito masa dakomai da kowa nagidan kafin malam yayi magana tuni sunshige gidan umma (sunan da ameera ke Kiran mamansu kenan)tana zaune à inda malam yabarta seganin katti tayi suna shigowa kafin tayi magana taga malam yashigo yana share hawaye  tambayarsa  tashiga yi "malam meke faruwane ? Cikin muryar kuka yace "maryam megidanne yace mufitarmasa daga gida wainnanma dakikaga sunshigo fitardamu da kayanmu

yasasu suyi,jeki kidauko mayafinki  juyawa tayi jiki ba kuzari tadauko hijab dinta dama kayansu nasawa agana must go suke dan haka dauka kawai tayi tunkafin takai ga nade katifarsu kattinan sunrigata wurgota kofar gida haka suka shiga wurgi da komai n'a gidan tsinke basu bariba daga karshe suka taso su malan bukar agaba shida iyalansa zuwa kofar gida bayan sunfitone sukaga kofar gidan cike da yan kallo manya da yara.makulli megidan yasa yakulle gidansa yawuce shida yaransa kota kansu be biba ganin jamaa nakara yawa akofar gidanne yasa malam bukar fara tattara sauran tarkacensu kama daga tukwane bokiti dadai sauran kayan tarkacen gida yakulle acikin wani buhu katifarma yasa igiya yadaure dama taji jiki yana gama daure katifar yadorama ameera ummansu kuma tadauki gana must go din kayansu tarike hannun ilham har zuwa lokacin kuka sukeyi dukansu harda ameera sabanin ilham datake tafaman sanaartata wato dariya malam bukar buhun kayan daya daure yadauka yace sutaho sutafi sudena zama agurin suna tarawa kansu mutane tafiya suka farayi dauke da kayansu suna kuka yaran garin kamar jira suke suka bisu abaya suna musu ihu sekace sunyi wani laifi kuma manyan gurin bawanda yakwabesu sabida makwabtansu  suntsanesu badan komaiba sedan kawai Allah yabasu ilham

haka suka cigaba datafiya yaran namusu ihu karshema suka fara jifansu seda sukayi nisa dagarin sannan yaran suka koma

Love you all 😘 maman yusuf

[1/28, 12:02] Zahra muhd mahmud□: *ALLAH GATAN BAWA*□□□□□□□□□□

_writting by Zahra Muhammad_



Tafiya sukayi me nisa sannan suka sami kasan wata bishiya suka zauna domin su huta. Har zuwa lokacin hawaye bedena zuba à idonsuba

Malam ne yakai dubansa fuskar ilham wacce ko baa fadamasaba yasan tagaji da hannu yayimata alama datazo kusa dashi.bamusu tamatso hannunta yarike yafara magana "ilham mu munyarda Allahne yayiki kuma yabamuke badan bayason daya daga cikinmuba kuma insha Allahu masu kinki nangaba se Sun huta à  inuwarki kiyi hakuri daduniya aduk yadda tazo miki .yafada yana zubda hawaye itako ko ajikinta danma tagajine danasan baabinda ze hanata darawa wani wata sarka yaciro awuyansa yadauramata awuyanta gami da fadin Allah ya albarkaci rayuwarki gaba daya suka amsa da ameen

Umma takatseshi tahanyar fadin malam kayi shuru haka Allah nan  kuma shine gatan kowa. Tana gama magana tamike  malam ne yace inazuwa kuma bayan hutawa mukeyi,tace wallahi kishin ruwa nakeji shine zan tsallaka titincan inga ko zan samo  ruwa, mikewa yayi yanafadin haba ina gurin shine ke zaki neman ruwa zauna inje inkawomuku. Haka tazauna badan ranta yasoba shikuma yatafi debo ruwan yanatafiya yana waiwayensu kamar  ze jiyo kuma sede yatafi sunanan zaune suka fara jiyo hayaniya abakin titin  gaban umma ne yafara faduwa tana tambayar kanta meke faruwa  takejin hayaniya haka kamar bazata jeba cam kuma tamike tanufi gurin tana zuwa taga anzagaye ana kallon wani abu karasawa itama tayi gurin yayinda bugun kirjinta yatsananta  tana karasawa gurin INNALILLAHIWAINNAILAIHIRAJIUN

Malan tagani kwance cikin jini mota tabugeshi kanshi ya rabe gida biyu ko baa fadamata ba tasan malam rai yayi halinsa yanke jiki tayi tafadi kasa sumammiya

love you all 😘maman yusuf

[1/28, 14:04] Zahra muhd mahmud□: *ALLAH GATAN BAWA*□□□□□□□□□□

_writting by Zahra Muhammad Mahmud_



Mutanen dake gurinne sukayo kanta domin Bata taimakon gaggawa  daukarta sukayi  sukasa amota tare da gawar malam  .sukuwa su ameera suna zaune Jin

shirun yayi yawane yasa ameera mikewa takama hannun ilham suma sukayo hanyar titin zuwansu yayi daidai  dazaasa ummansu amota dagudu ameera takarasa gurin tana Kiran ummansu  mutanenne suka juyo gareta  domin Sun fahimce mahaifiyartace har anhada daita amotar Sun fara tafiya sannan ta tuno da ilham dake can gefen titi  har zatayi magana sekuma tayi shuru sabida atunaninta ilham ba inda zataje harsuje sudawo tuna hakane yasa tamaida hankalinta kan ummansu wacce ke kwance rai a hannun Allah.

Asibiti akanufa dasu umma emmergency aka shiga daita yayin da malam kuma akayi mutuare dashi tagaban ameera akawuce dashi se alokacin hankalinta yakai gareshi wani gigitance ihu tasaki tayo kansa tana  ihu nurse ne suka riketa itako ihun Kiran baba take ahaka har aka shige dashi ciki duk wani me imani inyaga ameera se yatausayamata malam yarasu ga umma à emmergency rai  a hannun Allah

Dakyar nurse din suka rarrasheta tayi shuru abunka da yaro har wasa tafara. Kwatakwata tamanta da wata ilham hankalinta nakan umma tunda ance mata babanta yamutu. Secan da magariba aka fito da umma daga emmergency zuwa dakin 'yan paralyse domin itama umma asanadaiyyar faduwan datayi takamu da paralyse gabadaya barin jikinta daya yashanye har gefen fuskarta  .bayan ansa umma adakinne nurse suka kira ameera zuwa dakin likita, tabayoyi yafaramata kama daga sunansu, daga ina suke, awacce anguwa suke (dayake wainda suka kawosu  su suka bige malam. Daga cewa bari suyi sallah suka gudu ) sunansu tafadi sannan tafadi anguwarsu. Abinci likita yasa aka Bata daga nan yasa aka maida ita gurin ummanta gefen gadon tazauna sannan tabi jikin ummanta da kallo har zuwa fuskarta ganin yadda fuskar ummanta tasauya yasa tasanya kuka tana jijjiga umman tana fadin umma.gaba daya dakin bawan da betausayawa ameera da ummanta ba tananan har bacci yadauketa ajikin ummannata.

**********

Bata farkaba se dasafe se lokacinne tatuna da ilham dagudu tafito daga Dakin tana ihun Kiran ilham karo sukayi da doctor ganinta afirgicene yasa  yariketa yana tambayarta meke faruwa dakyar ta iya fadamasa dasauri yadauketa yasa amota suka tafi gurin dayake banisa amma koda zuwansu va ilham ba alamarta sede kullin kayansu juyo sukayi jiki bakwari bayan sungama duba ko ina nagurin ba ilham asibitin suka koma  ameera nata aykin kuka.

love you all😘 maman yusuf

[1/28, 20:26] Zahra muhd mahmud□: *ALLAH GATAN BAWA*□□□□□□□□□□

_writting by Zahra Muhammad mahmud_

*Page 24*

Suna isowa asibitin dakin da mama take suka nufa auna ta likitan yafarayi da mamakinsa yaga ba numfashi atare daita hankalinshine yafara tashi yana gudun kar ace ita ma babu ita awo n'a musamman yashiga yimata sede yamakaro Allahn dayayita yafishi kaunarta innalillahi wainnailaihirrajuiun itace kalmar dayake nanatawa zufa ce tashiga keto mishi ta koina dubansa yakai gun ameera wacce har Yanzu kukan rashin ganin ilham takeyi. Tausayinta ne yakamashi Jan hannunta yayi suka bar dakin bayan ya rufe gawar umman wasu nurse guda biyu yagani yabasu umarnin akai gawar umma mutuware

Office dinshi yashiga da ameera bayan Sun zaunane yafara magana " kiyi hakuri kinji kowa dakalar kaddararsa ketaki kaddarar Bata da kyau amma kigode Allah kinji .kai kawai tadagamasa sabida Bata fahimci meyake nufiba duba da kankantar shekarunta. Address dinsu yasake tambayarta tasanar dashi Jan hannunta yayi suka sake fita kai tsaye unguwarsu yaje da ita wani makocinsu yasamu mesuna malan sule bayan sungaisane yake tambayar sa shin koyasan wannan yanuna ameera dago kai malam sule yayi yakare mata kallo sannan yace yasanta yar gidan malam bukarce inafatande lafiya. Lafiya kalau likita yabashi amsa daganan likita yakoro masa bayanin abinda yafaru  harda mutuwar umma se anan ameera taji ummansu itama tarasu kuka tasamusu me tsuma zuciyar duk wani me imani shikanshi malam sule kukan yakeyi yakara da fadin jiya jiyannan mutanennan sukabar gidannanfa yanuna gidan ashe tsautsayine yafitardasu Kuka yasake barkewa dashi

likitane yakatseshi dacewa malam ba kuka zakayiba sonake ka kaini gidan megari inyimishi jawabi sabida asan yadda zaayi da gawarwakin. Tashi malam sule yayi gami da fadin biyoni muje gurin me garin. Kama hanya sukayi likita narike da hannun ameera ,akafa sukaje gidan megari dayake banisa bayan sungaisa dame gari sukayimishi bayanin abinda ke tafe dasu megari bakaramin girgiza yayi da labarinba duk da besan malam bukar amma yatausayawa rai shela yasa akayi agari akan jamaa suzo fada zaayi janaiza sannan yamike yabi doctor suka dunguma zuwa asibitin da isarsu akasaka gawarwakin amota bayan doctor yagama daukar hotonsu awayarsa sannan yayi cikecike a file dinsu. Kai tsaye kofar gidan megari akayi dasu Wanda yacika da jamaa cikin gida aka kaisu akamusu wanka megari yasallacesu aka kaisu gidansu nagaskiya

Wayyo rayuwa kowa nagurin yatausayawa wainnan bayin Allah se addua ake musu nasamun rahamar Allah.bayan anyi adduoine doctor yace zewuce sabida yanaso zetafi gida dan shi acikin garin kano yake ayki yakawoshi wudil. yanemi megari daya bashi ameera yatafi da ita dan zamanta agarin zedunga tuna mata danginta tana shiga damuwa.hakuri megari yabashi akan yayi hakuri zuwa Adan kwana biyu sabida karyayi gaggawar bashi ita daga baya danginsu nagurin iyaye suzo nemansu dan haka yayi hakuri aga abinda hali zeyi. Va ason ran doctor yatafi yabartaba wacce harzuwa lokacin daze wuce kuka takeyi ita ummanta dakyar ya rarrasheta bayan yamata alkawarin zekaita gurinta, naira dubu goma yakirgo yaba megari akan asiyamata  kayan sawa .yanacikin maganar ne  yatuna da kayansu nabayangari dan haka motarshi yanufa yaje yadebo kayan Wanda bawanda yatabasu sabida bawasu kayan kirkibane. Megari yaba kayan sannan yabukaci da à adanasu kodan gaba. Sallama yama megari yawuce, bayan tafiyarsa megari yasa akashiga da kayan cikin gidan shima shiga yayi rike da hannun  ameera yana shiga matanshi sukayo kanshi kowacce burinta yabata ita sabida me gari baya haihuwa dan haka dukansu basu da y'aya ganin inyace gawacce  yaba abin ze zama da rigima shiyasa yace dukansu yaba kowa nada iko akanta ameera kenan baiwar Allah .

jamaa ina labarin ilham ne ?

love you all 😘maman yusuf

[1/29, 20:45] Zahra muhd mahmud□: *ALLAH GATAN BAWA*□□□□□□□□□□

_writting by  Zahra Muhammad mahmud_

Iham tunda ameera tatafi tabarta take tsaye abakin titin bata matsaba tananan har kowa yawatse bata da alamar motsawa.

Gungun wasu almajirai sukazo wucewa sundawo daga yawon bara suna zuwa daidai da ita kawai seta bisu dan ita atunaninta gidansu zasuje tafiya sukayi metsayi

Sannan suka iso wani dan kauye dayake suna da yawa shiyasa basu lura da itaba tsayawa sukayi abakin titi da alama tafiyar dasukayi sunyitane dan samun ragin kudin mota baa kauyan zasu tsayaba wata motace kirar akori kura tazo wucewa dasauri almajiran suka fara tsaida motar

Motar harta giftasu tadawo da baya ina zuwa direban motar yatambaya. Kano suka hada baki gurin bashi ansa gyara parking yayi sannan yafito yabude musu kofar bayan motan dasauri almajiran suka fara darewa kan motar har sungama hawa ilham natsaye sabida ita bazata iya hawa da kantaba direbanne yawaigo yaganta atsaye atunaninshi tafiyarsu daya danhaka batare da Bata lokaciba yadauketa yasa acikinsu bayan yarufe kofarne yace dasu kudin motarsu naira hamsin hamsin basu musaba sukace Allah yakaimu lafiya zagayawa yayi yatada motar sukadau hanya

Tafiya sukayi medan tsayi sannan suka iso kano parking yayi agefen titi sannan yasakko yabudemusu kofa kowa inze sauka seya mika kudinsa harsuka gama sauka yarage saura ilham sauko da ita direban yayi sannan yamika mata hannu alamar takawo nata kudin kallonshi kawai take da lumsassun idanuwanta Wanda KO baa fadaba yunwa takeji

Ganin Bata da niyar magana yasa yakyaleta yashige motarsa yawuce yabarta agurin sukuwa dama almajiran sundade da wucewa.

Tananan tsaye har akafara Kiran sallar magaruba bata matsa a inda takeba amma zuwa lokacin tafara kuka sabida rabonta da abinci tun karin safe kukantane yajanyo hankalin wata mata meseda kunu da kosai kanta .kobaa fadamataba tasan yunwa ce tasa yarinyar kuka dan haka kunu tazubamata kunun da kosai taje gurinta tabata kallon ilham datayine yasa zuciyarta tashi sabida ilham inbanda warin rana da karnin miyau ba abinda takeyi ga wani zarni daya cika gurin asaka makon fitsarin datayi ajikinta

Seda me kunun tayi dana sanin bata kunun a robarta. Itako ilham nagani kunu bata tsaya tunanin komai takafa robar abakinta batadamu da zafin kununba tashanye tas sannan taci kosan ay tana gama sha takwanta agurin sebacci da gudu me kunun tabar gurinta domin lamarin ilham yafara Bata tsoro Yarinya dakyau kamar aljana sannan gata nakasasshiya ay bata bata lokaciba tahada kayanta tabar gurin

Love you all 😘maman yusuf

[1/29, 21:51] Zahra muhd mahmud□: *ALLAH GATAN BAWA*□□□□□□□□□□

_Writting by Zahra Muhammad mahmud_

*Page 26*

Tanan kwance agurin kowa yazo wucewa sede yamata fatan samun lafiya domin azatonsu mahaukaciyace

Tana gurin har zuwa karfe daya nadare se alokacin tafarka koda tafarka Bata tsorataba cigaba kawai tayi da tafiya duba da yadda garin kano dan musa me kwankwasiyya yawadatata da haske dan haka ilham tafiya kawai takeyi batunanin komai ba mutane sede jefi jefin motoci masu wucewa

Duk motar datazo wucewa nacikin motar kallon mahaukaciya sukemata bare yanzu data cire hijab dinta acan inda tasha kunu gashin kanta awaje yake gashi da yawa har gadon bayanta .tayi tafiya meyawa har tazo dai dai gadar yankura anan tayada zango ajikin gadar daga gefen titi baccine yasake dauketa agurin ba ita tafarkaba se da garin Allah yawaye shima tafarkane asakamakon hayaniyar mutanen dataji akanta bude ido tayi ahankali sannan tamike zaune tana kallon mutanen dakowa yatoshe hancinsa asakamakon warin kashin datakeyi domin kuwa kashi tayi akwance

Korarta mutanen suka farayi haka tamike tana kuka ko tausayinta basujiba wata bayarabiya harda marinta tana harkadata. Jinsaukar marin akumatuntane yasata sakin kuka me tsanani gami da kwasa da gudu ay tana fara gudun mutanen suka fara dariya sabida gudun abin dariyane koni naso nadara kawai dannasan wacece

ilhamne shine yahanani gudune irin naguragu tana fara gudun tafadi kanta yaji ciwo amma bata damuba burinta kawai tagudumma matar domin tunda tazo duniya baataba marintaba se ranar

Seda taci gudunta me isarta Wanda duk inda tawuce da gudun dariya jamaa keyi dan gudun abin dariya ne sannan ta tsaya tana haki yunwa tafaraji danhaka tafara neman abinci tahanya bin guriguri tana kuka kofar wani restaurant ta tsaya tana kuka to aciki akwai costomers suna brakefast acikinsu akwai Wanda yafara amai sabida ganin ilham dayawa daga cikikuma fita sukayi suka bar abincin ganin haka yasa matar me gurin tasowa takama ilham da duka bata barta seda tamata shegen duka sannan takoma ciki tadauko ruwan wankewanke ta kwaramata zuwa lokacin inka kalli ilham bazakace itabace sabida gaba daya fuskarta ta kumbura dan duka

matarce tafara balai dan ubanki gobe ma kikara zuwa kofar shagona ki korar min costomers mayya kawai wuce kibani guri. ilham nakwance agurin sabida jikinta yayi tsami ga yajin ruwan data watsamata yashigarmata ido da duk inda taji ciwo kuka kawai takeyi ganun ilham Bata da niyar tashi yasa matar janta akasa seda tayi nisa da ita sannan ta wurgar da ita cikin wata kwata Allah sarki ilham marainiyar Allah.

love you all 😘maman yusuf

[1/30, 21:26] Zahra muhd mahmud□: *ALLAH GATAN BAWA*□□□□□□□□□□

_writting by Zahra Muhammad mahmud_



*Bayan shekara biyu*

Zuwa wannan lokacin duk Wanda yasan ilham baze ganetaba sabida gabada takoma tamkar mahaukaciya sabida datti gashin kantama yadankare akanta kamar bata dashi

Rayuwace takeyi me cike da tausawa sabida ko abincin dazata ci yanzu yakoma sede tabi bola tasamu hakanne yasa duk Wanda yaganta yaga mahaukaciya

Har yanzu atiti take kwana ko kangon da baa gama ginashiba.

Yanzu shekarunta sha uku kuma awannan lokacinne Allah yakawomata jinin al'ada(wayyo Allahna)gaba daya jinin yagama bata mata jiki sabida jinin irin me rushing dinnanne ga azababben ciwon mara Wanda inya murda mata sede taita birgima har Allah yayayemata kuma koda jamaa sunga tana birgimar babu me bi takanta dan azatonsu duk acikin haukarne

Shiyasa yanzu warin datakeyi namusammanne ko ina tabi korarta akeyi babu me Jin kanta kuma lalurarta se abinda yakaru basauki sena Allah.

**********

Zuwa yanzu ameera na js2 sabida megari yamaida ita makaranta kuma har yanzu bata manta da yar uwarta ilhamba shiyasa kullum megari cikin bada cigiyarta yake sabida megari idan akwai abinda yatsana shine ganin ameera cikin damuwa  Sam baya kaunar bacin ranta dan inkaga ameera yanzu bazaka taba cewa ba yarsa bace kuma suma matansa kowacce cikin kyautatamata suke ba banbanci. Rayuwar ameera de se sonbarka matsalarta daya ce rashin yaruwarta ga doctor kullum cikin yimata ayke yake duk week-end kuma yana hanya dan yanzu sunsaba dashi kamar dan uwanta haka tadaukeshi shima kuma zallar tausayintane aranshi dakuma wani abu Wanda yabarma ranshi sezuwa lokacin dazata mallaki hankalin kanta.

love you all 😘maman yusuf

[1/30, 23:23] Zahra muhd mahmud□: *ALLAH GATAN BAWA*□□□□□□□□□□

_writting by Zahra Muhammad mahmud_

*page 28*

*Anwar  umar mutallib*

Dane ga shugaban kasar nigeria meci ayanzu wato Alhaji umar mutallib manumfashi.shekarunsa basu wuce 35 ba dane  daya tamkar dubu agurin mahaifinshi subuyu Allah yaba iyayenshi shine nafari agurin iyayenshi se kanwarsa mebinsa khadija wacce taci sunan mahaifiyar alhaji yasa suke cemata ihsan.

Mahaifiyarsu hajiya zainab ita kadaice agurin mahaifinsu shiyasa tazamana itace first Lady of Nigeria. Hajiya zainab macece kyakkyawa domin ita asalinta mutanen labanonce tsayawa fadin kyau irinna hajiya zainab zezama kauyanci sabida duk wani abu da ake kira kyau ga y'a mace takai karshenshi don kyannatane yake karasawa mijinta kaunarta.duk da kyau irinnata se Anwar yace bata iyaba domin yafita kyau nesa bakusaba mutumne shi miskili naajin farko kasaita gareshi kamar jinin sarauta  yayi karatunshi tundaga pramary zuwa secondry school a turkish school dake abuja inda yawuce da karatunshi na jamia a can kasar mascow har zuwa yanzu daya hada masters dinshi akan fannin petro chemical engenearing

Zamansa akasar waje yasa yafara neman mata tun yanayi kadankadan har yakai matakin daze hada mata uku akan gado daya kuma yayi amfani dasu batare daya gajiba sabida Allah yayoshi acikin jerin maza mabukata koya shaawa tamotsa masa baya iya hakura seya biya bukatarsa

Abokanshi nacan sunyi iya yinsu wajen ganin sunkoyamasa shan giya da coccane amma abin yaci tura domin shi baya kaunar abinda zegusar masa da hankalinsa. Anwar Wanda akafi sani da the most handsome domin haka kowa yake kiranshi sabida kyan Anwar ko ajinsin Larabawa da indiyawa se an tona zaa samu irinshi (kunsanme ? Duk kyansa bekai ilham ditaba)yana da gashi akansa metarin yawa yanayin gashinnasa tamkar arnav din kushi koya yamotsa bakinsa se beauty point dinshi yafitu sosai farine shi sosai kuma yanada tsayi amma bacanba sannan yanada faffadan kirji Wanda yake amurde hakan yasamo asaline asakamakon daga karfe daya keyi arayuwarsa baya kaunar komai sama da iyayensa da kuma kanwarsa kuma duk abinda zeyi yana bashi lokacine lokacin nafita shima yabar abin

misali inze gana dawani zece yabasa minti biyar tofa dazaran minti biyar tacika tashi zeyi yafice yabaka guri baya wasa da lokaci hakane yasa baya wasa da ibada duk iskancinsa baya barin sallah

Anwar mutumne shi Wanda beba soyayya muhimmanciba  ko matan dayake hulda dasu basonsu  yakeyiba  kawai for personal used yaajiyesu dan ko numbarshi basudashi

Ko bayan yagama karatu mahaifinshi yayi yayi dashi yadawo gida amma yaki kullum ansa dayace am on my way dady very soon tun mahaifin namishi uzuri har abin yafara Bata mishi rai dan haka yasa masu bincikamasa me Anwar yakeyine daya hanashi dawowa gida duk Wanda yasa binciken ansa daya suke Bashi neman mata yakeyi wannan batu bakaramin tada hankalin mahaifinshi yayi ba domin dede gwargwado suna iya bakin kokarinsu gurin ba yaransu tarbiyya dagashi har mahaifiyarsu kudi da mulki besa sunyi wasa da tarbiyarsuba hakannema yasa bekai ihsan karatu kasar wajeba don yana gudun zamani amma yau abinda Anwar zemasa kenan. Hakanne yafusatashi yakirashi awaya yana gaisheshi amma ko amsawa beyiba illa cewa dayayi cikin muryar fushi wacce Anwar bedauka dad dinsa yanada itaba. Duk abinda kakeyi anan inada labari kuma wallahi duk hukuncin dana dauka akanka ka kuka da kanka dan hukuncin baze maka dadiba danhaka duk abinda kakeyi kabarshi kabiyo jirgi ranar asabar kasauka a kano sabida nima zanje kanon wani taro semu taho abuja tare kuma wlh inbaka tahoba daga yau kanemi wani uban niba mahaifinkabane.yana kaiwa nan yakashe wayarshi yana huci

zuface tashiga karyowa Anwar kamar ruwa domin iya tashin hankali yashigeshi  jifa yashigayi daduk abinda hannunsa yakai kai yanayi yana fadin wayyo allahna wanne munafikine yahadani da dad. Hakade yagama dan matashin haukarsa yafara shirin barin kasar domin saura kwana biyu asabar din tacika.

**********

*Asabar*

da misalin karfe goma sha daya nasafe jirgin su Anwar yasauka  à filin jirgi na malam aminu kano tun kafin zuwan jirgin airport  din cike yake da security takoina sabida Anwar koda saukar jirgin shine mutum nafarko daya fara sakkowa wayyo Allahna sisters kuzo kutayani gani sanye yake cikin blue jins da farar shet sannan yadora katuwar rigar  sanyi baka wacce tsayinta yakai har guiwarsa kanshi yasa hular sanyi fara yayinda yanade wuyansa da irin wannan siririn abunnan

namaza(bansan sunanshi ba amma wani lokacin har rawani sunayi dashi)red colour inkuka ganshi bazaku so kudauke ido akanshiba domin yahadu saukowa yafarayi cikin tafiyarsa ta kasaita tunkafin yagama sakkowa aka shimfadamasa red carpet yasauko akai yaci gaba da tafiya har zuwa inda aka ajiyemasa motar daze hau wata bakar jeep ce kirar kamfanin Ford tinted ne gilas din motar murfin baya aka bude masa yashiga sannan akarufe sauran motoci kimanin guda goma sha daya suka rufawa motarsa baya yayin da gurin yacika da jiniya duk inda suka wuce kallonsu akeyi yayin da duk ababen hawa nakan titi suke basu hanya ahaka har suka iso govement house koda isowarsu wani kayataccen falo aka saukeshi Wanda ga abincinan na alfarma yaci iya cinshi yabar nabari jus kawai yasha sabida yaci abinci ajirgi nafeesace tayi sallama tashigo cikin falon y'a ce game girma gomnan jahar kano cikin ado nadaukar hankali se kwarkwasa takeyi Wanda shiwanda akeyi dominsa ko kallo bata isheshiba ita kuwa Allah ne yajarrabeta da sonshi tunda dadewa shiko basonta yakeyiba

koda tagaisheshi dakyar yaamsa suna nan zaune akayi ringing bel ita tabada umarnin ashigo wani sojane yashigo yadan kame gami da sarawa sannan yace ranka yadade  his highness yanason ganinka mikewa yayi kawai batare da ya amsaba yabi bayansa har zuwa wani falon. Mahaifinshine aciki tare da gomna suna hada ido da mahaifinsa yaji gabadaya kunya takamashi dakyar ya iya gaishesu cikin sakin fuska suka amsa har mahaifinnasa kamar bawani abu dayamasa gomnane yamatso yarungumeshi ajikinshi yajashi har kan kujerar dayake zaune yana fadin haba dan gidan dady yau gaisuwar daga nesace bazaazo jikin dadynba ko shide dukar dakai kawai yakeyi domin beson hada ido da mahaifinsa

bayan sundan taba hira megirma shugaban kasa yamike yace zewuce sabida yau yakeso yakoma abuja tashi akayi gaba daya harda gomna domin masa rakiya zuwa airport jerin gwanon motocine sunkai kimani guda talatin takoina jiniya ke tashi sukayoma shugaban kasa rakiya  ga garin akwai hadari sosai anfara yayyafi jamaa kowa yafake sekallon

Motocin akeyi kan kace me ruwa yabarke kamar da bakin kwarya

adede wannan lokacin ilham natsaye abakin titin ruwa nadukanta amma bata damuba sabida hakan sabontane tananan atsaye har motocin shugaban kasa sukazo wucewa

gomna da shugaban kasane abayan motar yayinda  Anwar ke zaune agaba shida direba.

karar jiniyar da ilham tajine yasata firgicewa dan haka Bata bata lokaciba gurin fara gudu gashi ana ruwa. Kamar ance Anwar yawaiga inda take haba mezeyi inba dariyaba dan abin gwanin bandariya dariya yake har rike ciki yana kwanciya  Jin dariyarsane yasa mahaifinsa kallonsa da gaggawa Wanda shi tuni yamantama da mahaifinsa yake tafe. Adede lokacin ilham santsi yakwasheta garin gudu tayi samasama tafado kasa haba Anwar ay har ihu ga kwalla data cikamishi ido dan

dariya  mahaifinsa mamakine yakamasa karara sabida tunda aka haifi Anwar betaba dariyar dazakaji sautintaba se yau

Anwar Wanda garin dariya har pointing dinta yakeyi batare dayasaniba hannunsa mahaifinsa yakalla dan ganin abinda yake yiwa dariya har haka  Allah sarki ilham yagani wacce zuwa lokacin harta mike tacigaba da falla gudunta na guragu ay Anwar nagani shima yacigaba da dariyarsa shiko mahaifinsa wani murmushi yasaki Wanda kai tsaye zamu iyan kiranshi namugunta  wayarshi yadaga yakira motar bayansu yabada umarnin adauko mishi ilham asa amotar Wanda Anwar dan dariya shibemasan mahaifinnasa yayi wayarba haryadena ganinta bedena dariyaba ahaka harsuka iso airport  ko gurin shiga jirgi anriga shigewa da ilham dan haka begantaba ahaka harsukayi sallama da gomna suka shiga jirgi  gurin zamansu daya da dadinsa amma koya yatuna yadda ilham tafadi har fadowa yake akujerarsa dan dariya sude security se kallon abin mamaki sukeyi  itako ilham tunda akadaukota amota take bacci sakamakon heater dake kunne amotar har akasata ajirgi bacci take  shiko mahaifin Anwar kallonshi yayi fuska dauke da murmushi yace aransa my son kenan ay dariya yanzu kosomata

love you all 😘maman yusuf

[1/31, 12:46] Zahra muhd mahmud□: *ALLAH GATAN BATA*□□□□□□□□□□

_writting by Zahra Muhammad mahmud_

Da misalin karfe biyar na yamma suka Isa Abuja koda saukarsu motocine da jamian tsaro bila adadin suna jiransu karasowa sukayi suka shiga mota zuwa gida

Tun ajirgi dady yaba wani excord dinshi umarnin yakai ilham wani guest house dinshi kuma yatabbatar yasamo matar dazata kula da ita dan haka koda suka sauka Anwar begantaba tafiyar dasukayi bata da tsayi suka iso gida tundaga get kowa ke sarawa har zuwa cikin gida suna shiga falon gidan mahaifiyar Anwar ce abakin kifa tana jiran shigowar gudan jinin nata dagudu yakarasa jikinta yarungumeta yana fadin imiss you mum somuch  ita ma hakan take fadamasa karasowar ihsan gurinne yasa yasaki mum yarungume ta itama dad ne yayi gyaran murya sannan hankalinsu yadawo gareshi

Mum ce tafara Isa gareshi tana murmushin dake kara fito da kyanta rugumeshi tayi sannan tace you are highly welcome my spouse dariya yayi sannan yayi huging nata back yana fadin bawaninan bayan duk kun manta dani ta Anwar kukeyi we are sorry tafadi gami dajan hannunsa suka haura sama

Anwar ma dakinshi ihsan taja hannunshi takaishi ruwan wanka tafara hadamishi sannan tace mishi bross kaje kayi wanka inka shirya seka samemu a dinning area na falon dady murmushi yayi mata kawai yashige toilet itako fita tayi tanata murna yau bross nata yadawo bakinta har kunne (amin afuwa banfadi ihsan ko yar shekara nawabace to me karatu ihsan shekarunta ashirin domin da fifting years Anwar yagirmeta)falo takoma tazauna zaman jiran mutanen gidan

Dukansu Sun hallara suna cin abinci sannan suna hirar yaushe gamo da Anwar amma dady bayasamusu baki momy tafuskanci hakan amma tabari sesun kebe ta tambayeshi meke faruwa hakane yasa shima kanshi Anwar yaki sakin jikinshi dasu

Suna tsaka da cin abincine Anwar yatuno ilham gurguwa habawa aywata irin dariya yafashe da ita harda rike ciki daga momy har ihsan sunfirgita daganin hakan banda dady dominshi yasan dalilin dariyar momy arude take tambayarsa lafiya sabida ita tahaifeshi amma tasan bata taba Jin sautin dariyarshiba seyanzu dafa shi tayi tana tambayarsa dan gabadaya tafirgice atunaninta aljanune suka shigar mata jikin shi

dakyar yaiya dena dariyar sannan yafara basu labarin abinda yasashi dariya tunda yafara labarin ihsan itama dariyar take momy ko murmushi tayi tace Allah yashiryeka Anwar yanzu dama dankaga gurguwane kake wannan uban dariyar wallahi kakiyayi kanka sabida hallittar Allahce bakyau hakan dakakeyi sabida kaima barawa kayi Allah yayi hakaba

Har zuwa lokacin dariyar taki sakinshi seda ihsan tayi katobara tahanyar cewa kai bross wallahi harna hango ka kaida ita amatsayin miji da mata tafada tana dariya wani gigitaccen mari yadauketa dashi kafin marin yasaketa yakara mata wani yadaga hannu zekara dady yarikemishi hannu shiko nuna ihsan yake da hannu yana

fadin ni saankine dazakiyimin wannan mugun fatan keko ihsan wacce irin kiyayyace tasa harkika hangoni amatsayin mijin gurguwa ni yafada yana nuna kanshi yayin da gaba daya jijiyoyin jikinsa suntashi haka gashin jikinshima yatashi idonshi yayi ja ba ihsanba hatta dady seda yatsorata daganin yanayinsa sabida one time yarikide dagudu ihsan tabar gurin tana kuka sabida kotsawa bross nata betaba yimataba Amma shine yau harda marinta daga yimasa wasa kuka tasake rushewa dashi

shiko ta maman tsaye se huci yakeyi momy ce tafara magana cikin sigar rarrashi haba my son meyasa haka wasa fa takema inbanda abinka taya zaka auri gurguwa wacce basake ganinta zakayiba  don Allah karage wannan fushinnaka shiko dady kallonsa kawai yayi yace ka kyauta Anwar you Will pay for it kansa yagirgiza yashige daki momyce tashiga yimasa nasiha sosai seda taga yasauko sannan tace yaje yahuta itama tabi megidanta daki

love you all maman yusuf

[1/31, 17:10] Zahra muhd mahmud□: *ALLAH GATAN BAWA*□□□□□□□□□□

_writting by Zahra Muhammad mahmud_

*this page is dedicated to Zahra Muhammad hausa novels group thanks you all am really appreciated*

Tunda daga wannan rana Anwar yafita harkar kowa agidan kamar yadda kowa yafita harkarshi ko momy tadena bi takanshi sabida dady yamata bayanin abinda yake aykatawa a mascow.

Kuma dady yashaida mata wlh seya dauki mummunan mataki game da abinda ya aykata

Yau lahadi Wanda yay dede da sati daya kenan da zuwan ilham abuja. tun karfe goma dady yashirya yafice agida tare da excord dinshi bazame ko inaba se gidan dayasa akai masa ilham gidan akwai tsaro sosai kai tsaye yashiga falon gidan tare da excord din daya ba alhakin kulawa da ilham wata dattijuwa suka samu zaune afalon wacce shekarunta basu wuce hamsinba matar kallon farko zaka mata kagane tanada kirki matar mesuna inna ladi jiki nabari tasauka akujera tana mikawa dadi gaisuwa Cikin mutunci yaamsa gaisuwarta sannan yasami guri yazauna bayan yazaunane yabada umarnin akawomishi ilham

Domin yaganta  inna ladice tashiga daki tafito rike da hannun ilham wacce ko dawasa akacemaka itace bazaka yardaba sabida tin lokacin daaka Daukota ake aykin gyarata asatin datayi a abuja har wata kiba tayi ga haskenta daya fito Wanda ada datti yaboyeshi gashin kanta har kusa da duwawunta yasha gyara bakamar da daya dankareba sanye take da Riga da siket na kanti Wanda suka kara bayyanar da kyanta sede harzuwa lokacin miyau nanan kamarda da sauran lalurorinta

koda aka fito da ita dady yayi matukar mamakin ganinta ahaka sabida betaba kawowa ransa akwai wani mahaluki afadin Nigeria daze gwadawa Anwar kyauba segashi yagani atattare da ilham baiwar Allah azuciyarsa yafara magana yana fadin inbanda iskanci irinna Anwar wannan ay baabar dariya bace sabida duk kyan dayake takama dashi wannan tafishi matsala dayace kawai lalurarta yanacikin wannan tunaninne aka zaunar da ilham agabansa dagowa yayi yakalleta cike da tausayawa itako se dariya take mishi hadi da gwarancinta Wanda ko baa fadamasaba gaisheshi takeyi yayin datake magana shikuma miyau yashiga ambaliya ko afuskar dadi babu alamar kyamatarta illa tausayamata dayayi juyawa yayi game kula daita wato inna ladi dan tayimai karin bayani

kara rusunawa tayi sannan tafara magana ranka yadade a iya zamana da yarinyarna nafahinci ba mahaukaciya bace kawai dolancine da ita domin har biro da takarda take rubutu bide bansan metake rubutawaba amma nasan duk dan makaranta yaga rubutun zeiya karantawa jeki kawo min rubutun inji dady mikewa tayi taje tadauko takardu wainda yawansu yakai goma daya bayan daya dadi yashiga dubasu abu dayane arubuce duka ajikin takaddun wato

*ilham shetima bukar*dady yayi matukar mamaki kobaaceba yasan sunanta kenan amma daya gwada seyace ilham bukar shetima dasauri tadaga hannu alamar itace kamar yadda takeyi amakaranta dariya duka sukayi  anan suka gane sunanta amanarta yakara dankawa inna ladi sannan ya umarceta data share wa ilham miyan bakinta zedauki hotonta  haka kuwa akayi inna ladi harda sake shafamata hoda tasamata jambaki wayyo Allah naso ace kuna gurin kuga yarda ilham tahadu ko kusa bame ganinta yayi zaton badaga indiya takeba dasauri dady yamata hoto kala biyu daya tasoma dariya wacce tabayyana hushiryarta me matukar kyau yayin da beauty point dinta shima yafito  intakaicemuku ilham tayi kyau matuka

bayan yagama daukar hotontane  yamike yamusu sallama yawuce.

koda isarsa gida hutawa yayi bayan yayi sallah yasa momy takiramishi Anwar da ihsan bayan sunzo dady ne yafara magana dacewa abinda yasa nataraku bakomaibane illa akan Anwar gaban anwarne yafadi azuciyarsa yace shikenan tafaru takare  muryar dady ce tadawo dashi daga tunanin da ya fada inda dady yadora dafadin Allah yasani tun ashekarun baya nake umarta Anwar daya kawo matar dayakeso domin yayi aure  amma yaki to hakanne yasa nidakaina nazabo masa wacce nake ganin tadace dashi ba Anwar ba hatta momy seda tafirgita dajin batun itako ihsan fadi take aranta Allah yakara  dasauri yadago yana duban dady amma yakasa magana sabida zafin da zuciyarsa kemasa dady ne yaci gaba nasamomaka matar aure diyar mutunci sede yarinyace karama dan shekarunta basu wuce 14ba what inji momy takatse dady tahanyar cewa haba alhaji me yar  14 years zatayi agidan aure dan Allah kabar wannan maganar shide Anwar nashi ido dan yasan dady baya magana biyu amma azuciyarsa jiyake dama shi aljanine kawai yatashi yabace dady yaci gaba kuma nan da sati biyu zaa daura auren ba wani shagali zaayiba kawai daurin aure zaayi shagalin zaa dagashi zuwa lokaci namusamman. hawayene suka fara ambaliya a kan kyakkyawar fuskar Anwar. dan bakinciki yazaayi yana mazaunin dan shugaban kasa Wanda ahalin yanzu ankai sunanshi majalisar tarayya  ta sanatoci da  ta wakilai akan su tantanceshi zaa bashi mikamin ministan man petur na kasa amma ace bikinshi bashagali sekace wani mara gata kuka yaci gaba dayi dady ko kallonshi beyiba ita ko momy tundaga kallon fuskar megidan tasan bayason wargi dady ne yadauko wayarshi yanuno hoton ilham yamikama momy yana murmushi yace  ga hoton surukartaki dasauri momy taamshi wayar tafara kallon hoton aybatasan sanda tarungume dady ba tanamishi godiya fadi take gaskiya kaiya zabe karfa kasa jamaarka sufarayi dakai tahanyar cewa se kyawawa kuke aure murmushi dady yakarayi yace wato naiya zabe ko  ihsance taamshi wayar ahannun momy  wani ihu tasaki gamida rungume yayannata Wanda tamanta fada sukeyi fadi take bross dady yagama yimaka komai tunda ze aurama wannan hurulinin  dan Allah kalli hoton kagani da kamar baze kallaba amma se yadaure yakalla danyaga wanne kyaune wannan dahar yafi nashi da na momynshi kallon hotonyayi dasauri yamike yana fadin subuhanallah wani matsanancin farinciki ne ya ziyarceshi  dagudu yakarasa jikin dady yarungumeshi yana masa godiya intakaicemuku Anwar harda yar kwallarsa ta farinciki godiya ko

zuwa yanzu ilham nanan apart din su momy domin koda yayiwa dady mgn kin amincewa yayi sabida momy tafadamasa abinda yayiwa ilham din dan haka dady yaki amincewa.

inna ladi yadawo itama gidan inda dady yasa akawaremusu daki ita da ilham tun zuwan inna kulawar ilham tadawo hannunta sosai take kulawa da ita.

ilham wacce ke dauke da ciki natsawon watanni hudu amma kaf gidan bawanda yalura tana da ciki domun cikin ko kadan benunaba illa jikinta dayabi zuwa yanzu takara kiba sannan ga wani fari datayi kuma cikin Allah yasa bame laulayi bane duk chanjin datayi jamaar gidan Sun Alakanta hakan da Jin dadi da kwanciyar hankalin data samu  baiwar Allah kenan cikin na motsi amma ita ina ko ajikinta

tunda inna ladi tazo tsawon wata biyu kenan Anwar besake samun damar zuwa gurin ilham ba tsawon watannin kuma besata a  idonshiba hakan bakaramin dadi yamasaba amma dazaran yayi mafarkinta burinshi yaje gareta amma ba hali sede yahakura

ziyara fadar shugaban kasa tashirya  inda zasu kai ziyarar ayki natsawon watanni biyar à kasar amurka inda acikin tawagar shugaban kasa harda ministan petur wato Anwar  dashi kanshi shugaban kasar.

ranar monday suka daga zuwa america suka bar gida cike da kewarsu zuwa yanzu momyce ce shugabar gida yayinda aykinta na office yakaru Bata samun zama agida

Koda zasu tafi seda dady yace anwar yaje yayi sallama da ilham amma yaki zuwa. Wanda shi dadyn besan bejeba

*BAYAN WATA BIYAR*

Cikin ilham yatsufa haihuwa ko yau ko gobe kuma dama tun zuwan inna takoyawa ilham wanka dakanta danhaka ita take wankanta duk da ba fita takeba amna inna tace gwara tadunga yima kanta dan tasaba dan haka har yanzu bawanda yalura dacikin jikinta amma fa tayi wata irin mahaukaciyar kiba wacce momy tace zata kira doctor yadubata anya kibar ta lafiyace kuwa  dan tunaninsu ko bata da isasshen Jinine ajikinta dan gashi har wata danyacewa tayi

yau da magaruba tawagar shugaban kasa suka iso  Nigeria dan haka kai tsaye gida aka fara rako shi sannan kowa yakama gabansa

Afalo yazauna bayan yayi wanka yaci abinci gaisawa yafarayi da duk mutanen dake cikin gidan ganin bega ilham bane yasa yatambayi momy hajiya ina yatane murmushi tayi sannantace inna taje tazo da ilham

agaban dady tazaunar da ita ganinta seda dady yafirgita  domin akalla inbata fishi kibaba toko baze fitaba mamakine yakama dady yace hajiya ilham sha kafashe kuke batane aa alhaji nima dayake bana samun zama wlh banluraba  amma gobe nace zamu kira doctor yadubata fada dady yarufe momy dashi tainda yashiga batanan yake fitaba itade hakuri kawai take bashi ana cikin haka Anwar yayi

sallama yashigo yasamu guri yazauna koda yaga ilham bakaramin tsoro tabashiba haryake tunanin anya ba aljana bace kuwa to inba aljanaba to tana da aljanu  dady ne yakatse mishi tunani incainda yace maza yakira doctor yazo yanzu numbar doctor akashe take dan haka dady yace Anwar yadauki ilham sutafi asibiti

mikewa yayi yana kunkuni shifa antakura masa

ilham wacce tun laasar mararta kemata ciwo amma dayake ba baki takasa shedawa kowa  to yanzuma datake gaban dady mararce kemata ciwo.

isowar Anwar gurinta yayi dede da karuwar ciwon dan haka da sauri tarike kafarshi tana kuka. hankalinsu ne yatashi  ganin yadda jikinta kerawa ga gumi daya gama jikata siket ne ajikinta irin me tattararnan kamarde irin na yan makaranta me falau dinnan dogo har kasa ba fant ajikinta dan tashiga bayi taga zaki yazubo yabata fant din sekawai tacireshi abayin fitowarta kenan inna taje ta kirata tagaida dady.

wani nishi tafarayi gamida durkushewa agurin haryanzu tana rike da kafar Anwar. tsawa dady yadakamishi akan yadauketa yamika hannu ze dauketa sukaji kukan jariri akasan ilham basu gama yanke shawarar abin yiba sukaji kukan yazama biyu haa ay da sauri dady yabar gurin innace takarasa kusa da ita tadagata daga durkushen da tayi ikon Allah ilham tahaifi yara biyu duka maza Anwar yakai dubansa kan yaran wani farin cikine yalullubeshi dakyar momy ta turashi waje  suka shiga aykin gyara mejego dayaranta kafin goman dare komai yayi normal kamar ba ayi haihuwa agidanba  momyce tadauki yaran tana kallo hawaye nazuba a  idonta tabbas base anfadamataba  wainnan yaran jinin anwarne domin Bata inda suka rabu dashi kamarsu daya mamaki takeyi tayaya har Anwar yasamu damar kusantar ilham har tasamu ciki tahaihu kai dubanta tayi kan ilham wacce gabadaya tasace dama kumburin na cikine tausayintane yakama momy  ajiye yaran tayi tarungume ilham tana hawaye dady ne yayi sallama yashigo dan yayi jiran akaimishi yaran yaji shuru shikuma yakosa shiyasa yazo dakansa kan kujera yazauna aka miko masa yaran  seda kwalla tazuboma dady tafarinciki yayi mamakin yadda yaran suka dauko Anwar sak addua yayi musu sannan yamike dasu a hannunsa yatafi dakinshi danba karamin so yakewa jikokinnasa

shiko Anwar yana bakin kofa yanaso yashigo amma yanajin kunyar haduwa da dady 😀gabahaba ay abun da kunya  Anwar.

*to fans dun Anwar ga ranarku kuzo kuraka Anwar yaga yaransa*

maman yusuf

[2/6, 16:54] Zahra muhd mahmud: *ALLAH GATAN BAWA*□□□□□□□□□□

Zahra Muhammad mahmud

*page 45-46*

Anwar nanan tsaye ihsan tafito taganshi yana leke dariya tasoma yimishi kiranta yayi yatambayeta dady nacikin dakin aa tabashi amsa dan haka with confidence yashiga dakin guri yasamu yazauna yana sosa keya momy takalleshi tana murmushi tace Anwar kenan angon karni ko shekara ilham batayiba Sega yara amatsayinta nawacce bakaso keyarshi yaci gaba dasosawa yana. Murmushi kalle kalle yafara yanason gamin yaransa danshi bata ilham yakeyiba shide burinsa yaga yaransa tare da fatan Allah yasa shi suka biyo

Momy ce talura da yanayinshi tace babies din kake nemako kai yagyada mata suna gurun dadynka kaje dakinshi kagansu

Jiki asanyaye yamike yafuta dakin dady yashiga da sallama dan harga Allah yakosa yaga yaranshi sallamarsa dady yaamsa sannan yamasa izinin shigowa yaran n'a hannun dady har yanzu kuma dukansu suntashi amma basa kuka se wasa da kafafunsu sukeyi annadesu acikin tawul dan babu kayansu dan baasan da cikinsuba bare atanaji kayan samusu

Gaida dady yayi cike da Jin kunya dady yaamsa masa fuska asake sannan yace Anwar kaga tashin hankalin daya samemu ko ashe ilham da ciki tashigo gidannan kai amma Wanda yamata wannan abu be kyautaba ninarasa yadda zan bullowa lamarin dady yafadi yana kallonsa dan yanaso ne yaji me Anwar zece shiyasa yace haka

Kan Anwar ne yadaure ganin daranshi dady nashirin shegantamasa yara dasauri yakalli dady sannan yafara da cewa dady wlh yaranane nine mahaifinsu  dady yace banganeba kana nufin kasan da cikin kenan amma baka fadawa kowaba nibansan tana da cikiba amma tabbas yaran nawane dariya dady yayi sannan yace taya bakasan da cikiba sannan daga ganin yara kace nakane kace kowama ze iya kama dan wani yace nasane

Anwar ganin dady da gaske yakeyi yasa shima yakara zage damtse wlh dady dagaske nakeyi nine mahaifinsu sabida ninafara sanin ilham yafada batare da shayin komaiba salati dady yayi sannan yace anya Anwar baka fara shayeshaye ba kuwa taya zakacemin haka bayan baku taba kwana guri dayaba. Habawa Anwar kamar jira yake yafara rantse rantse yana shifa yaranshine kuma bawanda ya  Isa yahanashi yaranshi shi wlh yaransane zuwa lokacin har yamike tsaye kamar meshirin yin dambe bakaranin dariya dady yayiba sannan daga karshe yayarda da Anwar din dama kuma gwadashi yayi danko mahaukaci yaga yarannan zece Anwar ne ubansu

mika masa yaran dady yayi yace yamusu huduba bayan yagama musu huduba yaci gaba da kallonsu yana hawayen farincikin yanajin son yaransa naratsa zuciyarsa

Wayarshi yadauka da niyar daukarsu hoto seyaga ba kaya ajikinsu betsaya tambayar komaiba yamikawa dady su yajuya da sauri yafita excode dinshi namaramasa baya mota sukaga yanufa danhaka suka gane fita zeyi kankace me kowa yashige mota cikin shirin kota kwana suka fice daga gidan

jin karar jiniya ne yasa dady yagane Anwar fita yayi ko  ina zashi oho momy ce tashigo dakin tsiya tasoma yiwa dady tana cewa kode shine angon karnin dariya yayi sannan yakwashe yadda sukayi da Anwar yafadamata momy dariya harda kwalla

daukar yaran momy tasake yi tana kallonsu sannan tace alhaji kaga ikon Allah ko. Wlh son yarannan nakeyi kamarni na haifesu rungumeta dady yayi gaba daya ita da yaran yana fadin mugodewa Allah shiyabamu  hakane inji momy

shiko Anwar yawo yadunga yi à garin abuja har yasamu wani baby care suka shiga dakanshi yadunga zabarma yaranshi kaya kowanne iri daya motoci guda biyar yafita dasu amma bawacce boot dinta becika da kayaba yabiya kudin suka nufi gida sukansu masu shagon se mamaki sukeyi zuwan Anwar shagonsu dan ba boyayye bane kowa yasanshi

misalin shadaya darabi su momy suka ga se shigo da kaya security sukeyi kamar hauka basuyi musu mgnb

har suka gama sannan Anwar yashigo

tambayarshi momy tayi wannan kayanfa na yaranane yabata amsa mamaki sukayi daga momy har dady ihsan ce tafara bude kayan wow kawai take fadi daga karshe yashiga tayata suna shigar da ayan dakin ilham tunkafin sugama tuni inna tadauki wasu kaysn sanyi farare tashirya yaran aciki bayan ansamusu Pampers

koda Anwar yashigo yagansu bakinshi yaki rufuwa daukarsu hoto yadunga yi awayarsa gashi yaran sunbude ido gwanin shaawa gasu identical twins ko ganesu bazakayi ba sekalura dazaran da inna tadaura musu itama tabanbancesune yayinda ta daga ilham bayab ta haihu anan taga daya akasa daya asaman dayan to nan tagane nakasan shine yafara fitowa

har yanzu Anwar kotakan ilham bebiba wacce ke kwance tana sharar baccin gajiya tayaransa kawai yakeyi

kan gari yawaye gaba daya hotunan twins yagama zagaya social media waya ko kama daga Anwar dady momy ihsan Sun fara amsata tun cikin dare duk yan taya murnane

dasafe inna tayiwa ilham wankan jego dan haka ta lura ilham na yoyon fitsari duba da tayi shinfidarta tajike hankalin innane yatashi

[2/7, 17:05] Zahra muhd mahmud□: *ALLAH GATAN BAWA*□□□□□□□□□□

Zahra Muhammad mahmud

*page 47-48*

Tunkafin inna tagama shirya yaran dady ya ayko adauko masa su bata bata lokaciba tagama tabadasu sannan tashirya ilham

Tagama kenan momy tashigo dakin kamar hadin baki Sega Anwar shima yazo ganin babies dinsa bayan Sun zauna inna tamusu jawabin matsalar data sami ilham momy gigicewa tayi shiko Anwar ko ajikinshi hasalima barin dakin yayi tunda abinda yakawoshi basanan

Dakim dady yanufa dan yasan sunacan sallama yayi yashiga bayan ya gaida dady sannan yadauki yaransa yana musu wasa harda yimusu selfie video shida dasu suna ta wuntsila kafafuwansu sama shikuma yanata musu wasa

Yananan zaune adakin dady momy tashigo afirgice ko sallama babu jikin dady tafada tasa kuka tana munshiga uku alhaji kar garin neman lada mukai kanmu wuta rudewa dady yayi yashiga tambayarta meke faruwa dakyar momy tamishi bayani

Shuru dady yayi yana girgiza kai sabanin Anwar Wanda bazaka ce yana dakinba. Se wasanshi yake da yaransa

Dady ne yamasa mgn dacewa Anwar bakaji lalurar data samu matarkabane.kallon dady yayi cikin sakin fuska yace naji dady allah yasauwake iya abinda zakace kenan inji momy wacce zuwa yanxu tafara fusata without care yace tomezance bayan hakan begama fadin abinda yayi niyyaba momy tadaukeshi dawani gigitaccen mari tace kana da hankali kuwa Anwar anya akwai imani a zuciyarka kuwa yarinya tasamu matsala tasanadiyyarka amma baka damuba

momy gaskiya kunfara takuramun akan lankwasasshiyarnan haba dawanne zanji da auramin miskiniyar dakukayi koko da abin kunyar daya sameni nazamantowarta uwar twins dina ni gaskiya kusauraramin haka haba yafadi batare dayajira mezasu ceba yasa kai yafice abinsa bayan yasauke yaran

momyce tamike da niyyar rukoshi dady ne yayi saurin kamota shikuma Anwar yakarasa ficewa

Kuka tasawa dady behanataba seda tayi shuru dankanta sannan dady yasharemata hawaye sannan yace banason matsalar Anwar tadameki zangasamiki Anwar dayardar Allah se yazo gabanmu yana kuka akan ilham kuma dama ban fadamiki bane jiya nayi waya dawani aminina nake fadamasa matsalar ilham shine yake

cemin yanada yaro babban likita akasar indiya acan yayi karatu kwarewarsa tasa suka daukeshi ayki ababban asibitin kasar dake Mumbai  kuma yakaranci fannin lalura irinta ilham danhaka gobe insha Allahu ilham da yaranta da inna ladi zasu wuce indiya zan gama musu komai ayau dinnan ko  ihsan banason tasan da tafiyar bare Anwar kinjiko

Farincikine yalullube momy takara rungume dady tana mishi godiya dady ne yaci gaba kuma wannan matsalar yoyon fitsari data sameta duk acan akwai likitocin cutar dan haka ba matsala insha Allahu Inde kudi da mulki na rana zasuyi akan ilham murnace tasake kama momy

Kamin rana gidan yafara cika da yan barka yaran kawai momy tabada umarnin afito dasu in ance ina mejegon sede tace doctor yahanata zama cikin hayaniya suyi hakuri

haka aka ci gaba dazuwa barka har dare

shiko Anwar tun fitarsa office yawuce yana shiga yafara tura video din dayayi shida twince a social media habawa jamaa sunkara gigicewa da kyan twince se fatan alkhairi ake musu

*washe gari*

koda safiya tayi Anwar shigowa yayi yagaida dady sannan yagaida momy  ga mamakinsa duk Sun amsa masa cikin sakin fuska

dakin mejego yashiga yatarar inna narike da yaro daya ilham nabashi nono dayan kuma nakwance akan gadon

ran Anwar ne yabaci ganin ilham nashayar mishi dayara azuciyarsa ya yanke shawarar daukomusu me renonsu daga london danshi baya kaunar ilham tashayar mishi dayaranshi

ganin nonon ilham awaje shine yatada masa da shaawa kuji mara kunya dan haka yashiga kallonsu yana lashe baki inna ce talura dashi danhaka ta ajiye yaron tafice karasawa yayi kusa da ilham yakai hannunsa kan nononta yafara wasa dashi itade kallonshi kawai takeyi tana murmushi

jin motsin mutum yayi abayanshi dasauri yajuya momy ce atsaye tana kallonshi kunyace takamashi amma ga mamakinsa momy murmushi kawai tayi masa sannan tace baban twince yau ba zuwa office ne gashi har t'en tayi mikewa yayi yakarasa kusa da yaran yanata kallonsu haka kawai yadunga Jin jikinshi yamutu daukarsu hoto yayi sannan yamusu vidéo abin mamaki yau harda ilham akama video momy mamakine yakamata gabin Anwar yaruko hannun ilham yanacewa maman twince pls ki kulamin da yarana sannan yayiwa twince Kiss yafice yana waigensu yana fita office yawuce dama shi ake jira yafita dan tuni jirgi na airpot yana jiran su ilham 😉

shiryata akasakeyi sannan inna tarukota momy kuma tarungumo twince security najan kayansu har mota

airpot sukaje harda dady arakiya yayinda security mutum ashrin dady yabasu sunanan tsaye har jirginsu ilham yatashi zuwa kasar india Wanda kosu su innan basu San ina zaakaisuba

acikin jirgi inna se wukiwuki take da ido acikin security akwai mata guda biyu sune ke rike da twince Wanda dady yarada musu suna sultan da sudeis

misalin karfe shida na yamma jirginsu yasauka akasar india inda suka tarar da cincirundon motoci guda goma suna jiransu kai tsaye wani kerar gida aka saukesu fadin abinda ke cikin gidan yayiwa page dinnan kadan gida de yahadu komai akwai harda masu  ayki

Anwar yataso daga office dawuri yau dan yau tunda yafita yarasa sukuni bawacce yake son gani irin ilham dan wani mahaukacin kewarta yake ayau dinnan dan haka yakosa ya Isa gida yasata a idonshi😉

[2/8, 12:08] Zahra muhd mahmud□: *ALLAH GATAN BAWA*□□□□□□□□□□

Zahra Muhammad mahmud

*Page 49-50*

Anwar na Isa gida part din sa yawuce wanka yayi yazura doguwar riga yanufi part din su momy

Dukansu suna zaune afalo yayi sallama yashiga gaishesu yayi kai tsaye yanufi dakin dasu ilham suke ga mamakinsa basa ciki kuma ba kayansu kanshine yadaure yashiga tambayar to ina suka shiga

Dasauri yadawo falon

Momy ina su ilham suka shigane naje dakinsu bangansuba

Dady ne yabashi amsa dacewa ay tunda na auramaka ilham nafahinci na zalinceka kuma zamanku tare tana cutar dakai shiyasa nazabi farincikin dana

Namaida ilham gaban iyayenta kaga kahuta ko my son

What!!!!!!

Inji Anwar haba dady ninacemaka tana zalintata dazaka kwasheta kamaidawa iyayenta kuma ma inmaidata zakayi seka hada da yarana gaskiya nibakamin adalciba kuma wlh bazan yardaba yafadi yana kumburo bâki

Dariyar momyce tamaida hankalinshi gareta azatonshi zatace wasa  suke

Lalle Anwar baka da kunya tunda har kasamu kwarin guiwar tsayawa agabanmu kana neman ilham matar dabakaso katsaneta cewafa kayi zaka iya kasheta sabida tsananin kiyayyarka gareta kobaka fada bane momy ta tambayeshi

Zuwa yanzu Anwar yafahinci iyayensa yan rainin wayone😀danhaka dole yanunamusu shidan zamanine

Cewa yayi haba momy wacce kiyayya kuma bayan har haihuwa ilham tayi kinga ba zancan kiyayya anan danhaka dan allah kusanar dani inda yarana suke yafadi yana durkusawa agabansu cikin fuskar tausayi

shewa momy tayi sannan tace dadina da gobe saurin zuwa to mun cinyesu kashakemu muyi amansu

Dady yamike yawuce daki batare dayace komaiba  momy tamike tabi bayansa suka barshi shida ihsan afalon

Ihsan dan Allah fadamini inda su twince suke da mamansu

wlh bross ban san inda sukeba nima zaman danayi anan tambayar danake musu kenan kuma desame answer suka bani dawacce suka baka inji ihsan

Iska ya fesar sannan yaruntse idonshi ranshi namishi kuna zuciyarshi kamar zata tsage. Azuciya yafara mgn haba dady meyasa zaku rusamin farincikina twince sune rayuwata amma kunrabani dasu ilham ninasan basonta nakeba amma zuwa yanzu inason ganinta. Wasu hawayene masu dumi suka gangaro akan fuskarsa tabbas yasan wannan shirin nadadyne dan yayi imani dady yafi kowa kinsa tashi yayi afusace yabar part din dakinshi yanufa yana shiga wayarsa yadauka yakira naseer awaya yana shaidamasa abinda ke faruwa

naseer seda yatausayamasa sabida twince kowaye mahaifinsu baze so suyi nisa dashiba  hakuri yadunga bashi yanacewa horone su dady sukemishi abisa wulaancin dayayiwa ilham Wanda yasan nanda dan lokaci zasu hakura sudawo mishi da matarsa sallama sukayi

*Bayan wata biyu*

Zuwa yanzu Anwar yatabbatar da ilham tamishi nisa gaba daya yazauce akanta ita da yaranta kullum cikin kallon hoton daya musu yakeyi

kuma har yanzu iyayensa sunki suce masa komai gameda ilham da yaransa

harga Allah yanzu yasoma tausayin ilham amma basonta yakeba( nace kuji wawa )

*Ilham*

acikin watanni biyunnan anyi nasarar tsaida miyaun datake zubarwa haka shima lalurar yoyon fitsari andade da maganceta dayake akwai kudi domin baabinda dady betana darmusuba

haka suma su twince kullum kara wayo sukeyi  abin gwanin shaawa kuma itama ilham yanzu tagane su amatsayin yaranta dan har wasa take musu

yaune aka saka ranar yima ilham ayki wajen ganin anmikar da kafarta dakuma hannunta wani injine zaa sata aciki na tsawon kwana uku ana kuma sa ran dazaran tafito dayardar Allah zata warke. Dan haka tun safe suke tawaya da inna da su dady tana fadamusu abinda ake ciki duk da shima doctor din yana waya da dadyn

tun zuwan dasuke asibitin doctor betaba kallon ilham ido cikin idoba sabida becika kallon mataba

yau anyi saa suna shigowa office dinshi idonshi ne yasauka anata afirgice yatashi yanakallonta badan komaiba sedan tsananin kamar datakeyi da mahaifinsa tirkashi wai waye doctor din ilham ne

Maman yusuf

[2/8, 17:49] Zahra muhd mahmud: *ALLAH GATAN BAWA*

Zahra Muhammad mahmud

*page 51-52*

Har suka karasa cikin office din doctor natsaye yakasa zama har seda inna tafara gaisheshi sannan yadawo da tunaninsa zama yayi yana cigaba da kallon ilham

Bayan yadauko file na ilham ne yakara lura da sunan dake rubuce ajiki ilham bukar shettima. Tabbas zatonshi yazama gaskiya amma zebar komai har zuwa ilham

tasamu sauki  rubuce rubuce yayi sannan yaba inna madarar dazata dunga ba twince nan da kwana ukun

Anshigar da ilham cikin machine dan haka inna direba yadawo da ita gida ita dasu twince zuciyarta cike da adduar Allah yasa adace.

*Doctor Adnan imam shetima*

Shine cikakken sunan doctor dake duba ilham dane ga alhaji imam shetima saurayine matashi Wanda shekarunsa bazasu gaza 35 ba shikadaine agurin iyayensa kallo daya zakama adnan kasashi acikin jerin kyawawan maza domin kyakkyawane na ajin farko bashida son hayaniya kwatakwata shiyasa beson zama à Nigeria. Mahaifiyarsa sunanta hajiya hauwa macece me kirki haka shima mahaifinsa Wanda yanzu haka suke zaune agarin kaduna tunbayan barinsu garinsu na aynihi wato meduguri asakamakon yakin daake a yankin

Adnan yayi primary da secondry schools dinsa duk agarin meduguri kuma Allah yaba mahaifiyarsadamar dauko jakar takardunsa shida mahaifinsa lokacin dazasuyi hijira dan haka kobayan zuwansu kaduna basu sha wata wuyar rayuwaba mahaifinsa yasamu ayki a nnpc kuma ana bashi albashi me tsoka shiyasa yanemar masa Abu zaria inda acanne yayi degree dinsa nafarko

Lifes move on mahaifinsa yazama hamshakin mekudi dan haka yakaishi kasar india domin yakarasa karatunsa n'a doctor acan

Duk da yawan tarin dukiyar mahaifinsa kullum cikin damuwa yake da bacewar dan uwansa bukar Wanda yanemeshi har yafidda ran ganinshi suko dama iyayensa yasan Sun mutu dan haka yake musu addua amma rashin sanin labarin kaninsa nasashi acikin damuwa dan so tari ze kulle kanshi adaki yaci kuka

Halin da mahaifinsa keciki yana dagamasa hankali har yakejin da yanada ikon cirewa mahaifinsa damuwarsa dayayi

bayan wasu shekarune mahaifinsa yafada harkar siyasa inda ananne suka hadu da mr président wato dadyn Anwar

Mahaifin adnan shine yadauki nauyin campagne din dady har kuma Allah yasa akayi nasara dady yaso yabashi minister naman petur amma yaki tun farko hawan dady mukamin Abban adnan yace bashida raayin mukamin amma shi ya yarda yadunga basa kwangila haka ko akayi ko lokacin auren Anwar baya kasarne yana saudiyya shiyasa be hallaci bikinba kuma shi baya hawa social media bare yasan wacece amaryar Anwar shide kawai dady yacemishi tsuntota yayi kuma sunanta ilham danse akwanakinannema yake shaidamishi Bata da lafiya shine yahadashi da adnan dan fannin yakaranta

Tsakanin adnan da Anwar basu San junaba dan iyayensune suke burin su hadasu Abota.

har kudi masu tsoka Abban adnan yasa gaduk Wanda yaga dan uwansa ko yaji labarinsa amma har zuwa yanxu bawani bayani yahakura yabarwa Allah

*cigaban labari*

twince koda suka daina shan nono basu damuba domin tun asalinsu masu hakurine shiyasa inna bata samu matsala dasuba

*Nigeria*

Anwar yanzu ko aski bayayi zuwa yanzu ko office yadena fita se mataimakinsane ke gudanar da komai.

da yadauka iya su twince kawai yakeson gani se yanzu yatabbatar da basu yake soba mahaifiyarsu yake da bukatar gani kuka da magiya yayiwa su dady ba iyaka akan sudawo masa da iyalinsa amma ko takansa dady bayabi ihsance kawai take tausayinsa take bashi shawara dayayi hkr komai lokacine shide sede yakalleta kawai amna bajinta yakeyiba  domin yanzu yagama yarda 100% ya kamu dason ilham Wanda ko kansa bayaso kamar haka burinshi su sanar dashi inda take dan yanemamata Lfy sabida bayason taji lbrn abinda yadunga mata abakin wani shida kansa yakeson shaida mata kuma yanemi yafiyarta amma su dady sunki bashi hadin kai. Ko abinci yadena ci sosai sede ihsan tamatsamasa yaci domin su dady gaba daya sunfita harkarshi

kuma kullum suna waya da inna sunajin halin da ilham take securityn da dady yahadasu dasu sune ke daukar twince ahoto suyima dady sending through WhatsApp dan haka baya kewar jikokinshi tunda kullum seya gansu

Anwar ne kadai ke haukarsa

*India*

bayan kwana uku yau ne zaa ciro ilham acikin machine din da akasata. tun asuba su inna suka zo asibitin suna jira.

Damisalin karfe takwas nasafiya doctor adnan yaciro ilham.

hasbunallahu wani imal wakil wala haula wala kuwwata illa billahil azim

ilham ce nagani tsaye akan kafarta hannunta daya lankwashe shima asake kai kubarni nakara yiwa Allah kirari

lalle Allah shine Allah kuma shine meyin yadda yaso Alokacin dayaso  babu meyiwa dan Adam baiwa se Allah

ganin ilham danayi yasa na kara tsoron Allah

dakafarta tafito inda su inna suke dakon futowarta doctor nabinta abaya

inna naganinta sujjada tayi ga Allah sannan takarasa da sauri tarungumeta

tabbas ilham bata manta innaba dan haka itama rungumeta tayi tana kuka

ihamce ke fadin Alhsmdulillahi Allah nagodemaka daka azurtani dasamun Lfy. inna seda takusan shidewa sabida Jin ilham namagana cikin muryarta kamar ana busa sarewa  rungumeta inna tasakeyi tana fadin lalle Allah shine abin godiya ilham

waige waige ilham tafara Wanda inna tafahimci yaranta take nema dasauri taja hannunta zuwa inda aka ajiye su twince dasauri ilham tasa hannu tadaukesu duka subiyu kuka takara fashewa dashi nafarincikin ganin tadauki yaranta da hannunta Wanda da sede amiko mata  kissing dinsu tashigayi kamar zata lashesu suko su twince se dariya sukeyi nace ikon Allah

doctor ne yashigo sannan yanemi guri yazauna yana murmushi yace to maman twince Lfy tasamu kuma se kuka nide karki koyama twince kuka sabida basayi murmushi tayi sannan tafara yimasa Godiya..

magungunan dazata cigaba dasha yabasu sannan yamusu fatan alkhairi suka hadayanasu yanasu suka wuce masaukinsu

maman yusuf

[2/9, 16:51] Zahra muhd mahmud: *ALLAH GATAN BAWA*

Zahra Muhammad mahmud

*page 53-54*

Tunda ilham tasamu sauki kullum suna waya dasu momy abin bakaramin dadi yayiwa dady ba momy ma ji takeyi kamar tayi tsuntsuwa taga ilham

Dady sunyi mgn da doctor inda dady yanemi daya nema masu ilham biza daga india zuwa saudiyya domin suyi umara

Ayko hakan akayi domin ilham basu kuma sati guda agarin india ba se asaudiyya

Tun isarsu garin madina ilham ke kuka na farinciki kwanansu shida amadina suka Isa makka

Ilham tayi addua sosai aciki kuwa harda Allah yabayya namata yan uwanta sabida inna tafadamata komai game da tsuntota da dady yayi shiyasa Bata da sukuni illa Allah yabayyanamata danginta

Tafiyarsu zuwa saudiyya tare da doctor adnan akayita

Dan haka yanzuma shi dady yawakilta akan yanema musu biza zuwa UK sabida yanason ilham taci gaba da makaranta acan

Dan haka adnan beyi wasaba yayi abinda dady ya  umarceshi

Koda zuwansu birnin london basuyi sati biyu ba adnan yakai ilham wata makarantar secondry tambayoyi suka mata Wanda seda sukayi matukar mamakin amsoshinta dan har inda basu tambayaba take kaimusu amsa lalle Allah me girma da daukakane gashi yaba ilham ilimin da bawanda yayi zato

Kudi dady sosai yasaki kamin ayiwa ilham certificate din primary da na junior waec domin a  ss1 akasata

Sosai ilham take maida hankali ga karatunta Wanda take ganin dashine zata taimaki iyayenta😭

So tari intadawo gida zata zauna tayi shuru Tana tuna wasu abubuwan dasuka faru wasu tamanta wasu kuma bata mantaba

Duk abinda anwar yamata nacutarwa tamanta shi sannan mutuwar iyayentama bata tunaba hatta auran da ke kanta seda inna tamata Karin haske akai amma fa

yanbiyu Tana matukar kaunarsu kuma tarasa dawa suke Kama itade tasan bada ita suke kamaba

kamannin anwar gabadaya tamantasu shiyasa ko tunaninshi batayi. kawai abinda tadaukarwa ranta shine ko waye baban su twince gaskiya baya kaunarta itada da yaranta Wanda Zuwa yanzu tanajin tsanarsa azuciyarta sabida tayi imani dayana sonsu dayazo inda suke musamman data samu lfy

*bayan shekara daya*

su twince sunyi wayo komai sunaci basu fiye damuwa da nonoba shiyasa inna tashaidawa momy momy tace ayayesu

zuwan daddy da mommy hudu gurin su ilham suna dubasu shima doctor Adnan yana yawan zuwa dubasu Dan soyake yabi aynihin tarihin ilham yasan wacece ita

Yanzu ilham na ss3 inda dady yace inta kammala ss3zata dawo Nigeria abun yayiwa su ilham dadi dan harga Allah  sungaji da zama akasar dabatasuba

Ilham tayi kyau matuka bame cewa ajikinta su twins suka fito tsayawa fada muku kyan da ilham tayi da cigaban datasamu page dinnan yayi kadan sosai dady yake sakar musu kudi

Twince koda aka yayesu basa rigima tafiyarsu sukeyi ko ina gasu tun suna yara sun taso da kaunar junansu dan ko kuka daya yakeyi se dayan yatayashi

*Anwar*

Kafin wannan lokacin anwar yakwanta a asibitoci daban daban afadin garin Abuja babu me ganinshi yaganeshi one time

kowanne likita yanabashi shawarar yarage damuwar dake zuciyarsa Dan hakan ze iya haifarmasa da ciwon zuciya dangama hawan jini tuni yasameshi asanadiyyar rashin ilham  shi yanzu bata yaransa yakeyiba shide ilham yakeson gani

momy tatausayawa halin dayake ciki har taso ta tona asirin su tsakanin da da uwa dakyar daddy ya lallabata akan tayi shuru ilham takusa dawowa dan koshi dadyn dauriya kawai yakeyi amma yadamu da halin da anwar yake ciki shinema silar dayasa yace ilham intayi ssce tadawo da soyayi tayi university dinta acan

ihsan kullum itama setayiwa su daddy kuka akan sutausayawa bross nata sufito mishi da ilham kar yarasa rayuwarsa hakuri kawai daddy ke bata dan tabbas se ilham tagama school zata dawo

zuwa yanzu ancire anwar amukaminsa sabida mulki seda lafiya shi kuma yarasata adalilin ilham.

*yau 22-09-2016*

ayaune doctor moneer yake dawowa Nigeria bayan yakammala karatunshi na tsawon shekaru biyu dayashafe yanayi

a airport iyayenshi da yan uwansane sukaje tarboshi

beso hakaba danshi yaso ace driver aka turo mishi da babu abinda ze hanashi wucewa wudil gurin ameera Dan yakosa yakaimata albisheer dan zuwa yanzu har hoton su twince da video din da anwar yamusu tare dashi duk yanadasu awayarsa

bayan isarsu gida wanka yayi yaci abinci sannan aka zauna zaman hirar yaushe gamo. nanne dadynsa yafara mishi zancan yafito da mata ko yar wanene yadauramasa aure shi baruwanshi dacewa se yar babbangida shide yasamo me tarbiyyaa da  asali

murmushi moneer yayi sannan yace insha Allahu daddy kwanannan zankawo maka matar danakeso. Allah yanuna mana lokacin. Inji dadynsa ameen suka amsa gabadaya

key din motor daddy yadauka zefice da sauri daddy yace ina zuwa haka daga dawowarka ko hutawa bakayiba kodan kaga saukar safiya kayi shine zaka fita yawo Kai yasosa sannan yace dad gurinta zani  yana fadi yafita dagudu Dan bayaso suhanashi zuwa

suko su dadyn dariya kawai sukayi gamida yimishi fatan alkhairi

Gudu moneer yake amma gani yake motar bata sauri

yakosa yasa ameera a idonshi wacce yasan zuwa yanzu takara girma

 to anan semuce safe trip moneer.

[2/10, 23:31] Zahra muhd mahmud□: *ALLAH GATAN BAWA*□□□□□□□□□□

Zahra Muhammad Mahmud

*page 55-56*

Yayi tafiya Medan nisa sanna ya iso wudul. Gidan megari yanufa lokacin megari yana fada.

Koda zuwansa gaisuwa yayi  yasamu guri yazauna. Megari Wanda tun zuwan moneer gurin bakinshi yaki rufuwa yace idonka kenan manniru bakin turai tashi yayi yayiwa yan fada sallama yaja hannun moneer zuwa cikin gida

Matan megarine azaune atsakar gidan suna hira  ganinshi da moneer yasa suka fara tsokanarsa da cewa seyau ake ganinka gaishesu yayi sannan suka zauna shida megari akan tabarma suna hirar yaushe gamo

Ganin yakusa awa dazuwa amma bega ameeraba yasa yatambayi inatake inna asabe (uwargidan megari)ce tace taje makaranta amma yanzu zaka ga tashigo ay lokacin tashinsu yayi

Tana rufe baki ameera tayi sallama tashigo ganin moneer datayine yasa ta tsaya tsak shima numfashinshine yakusa daukewa sabida ganinta megarine yace to ki karasomana kintsaya daga nan shigowa tayi jikinta asake kuma har yanzu idonsu nakan juna

Megarine yayiwa matansa nuni dasu tashi subasu guri dan gama sun manta dasu agurin

Dakunansu suka shige harda megarin

Inda ameera tamaye gurbinsa gurin zama a inda yatashi itace tafara dauke idonta akansa sannan tahura mishi iska a fuska shima yadawo hankalinshi

Gaisheshi tayi cike dajin kunyarsa dan zuwa yanzu itama tanason moneer duk da kankantar shekarunta

Amsawa yayi cike daso da kauna be bata lokaciba yaciro wayarsa yacemata albishirinta goro tabashi amsa miko mata wayar yayi bayan yanuno hoton ilham da Anwar

Dasauri ameera take kallon hotunan tabbas wannan ilham ce sabida duk sauyawar dazatayi bazata taba mancewa da itaba sabida akwai shakuwa sosai atsakaninsu. Cakume moneer tayi Tana kuka Tana cewa Don Allah aina kaga yaruwata kataimakeni kakaini gurinta Tana jijjigashi

jin kukantane yasa su megari fitowa suna tambayar meke faruwa dakyar moneer yasamu tasakeshi yayiwa megari bayani

Labarin yamusu dadi sosai kuma suma sunga hotunan

Baabinda yake daure musu Kai irin auran datayi harda yara kuma dan shugaban kasa

Ameera wacce har yanzu kuka take kallon hotunan su twince takeyi tanajin sonsu azuciyarta Wanda tasan koba komai yanzu suma sun Kara yawa akan da dasuke su biyu abinda yake daure mata Kai shine ganin ilham datayi fes ba miyou wato hakan na nufin tawarke Keenan kokome

maida hankalinta tayi ga tambayar dame garin takewa moneer dacewa manniru mutabannan bamu da ikon zuwa gidansu sabida sunfimu taya Kake ganin zamu je garesu dasunan ameera yar uwar ilham ce

shuru yayi  yana tunani karshe yasamu mafita

Wayarshi yaciro yashiga instagram yayi searching sunan Anwar ayko nan take yafito hoton ilham nema a dp following dinshi yayi sannan shima yadauki ameera hoto yadora a dp nashi sannan yayi status dacewa Don Allah jamaa duk Wanda yaga yar uwata koyasan inda take yataimakamin yasadamu munrabu ne tun muna yara  sunanta ilham bukar Shetima

yana gama rubutawa yayi updating hoton ilham amatsayin wacce ake nema

yamusu bayanin abinda yayi kuma yabasu tabbacin mijin ilham yana muamala da instagram sosai nan da yan lokaci zegani dan haka sujira sugani

*Anwar*

Wanda ke kwance akan gadonsa rike dawayarsa yana kallon hotunan ilham yaji wayar tasa tayi kara alamar yasamu sako da kamar baze dubaba sede kawai yaduba seyaga wanine mesuna moneer yayi follow dinshi a instagram  sannan kuma yayi tagging dinshi da kamar yashare seyaji yanada shaawar yaga wanene moneer din shiga yayi instagram din mikewa yayi dasauri ganin hoton dake kan dp din moneer din dasauri yayi accepting dinsa sannan yashiga kan hoton dayayi posting tabbas ko a bacci aka tasheshi ze iya banbance tsakanin ilham da ameera sede Abu dayane da ya yarda dashi sunyi matukar Kama dajuna

status din yasoma karantawa mikewa tsaye yayi dasauri yana Kara karantawa dankari ay ji yayi duk wani ciwo najikinshi yawarke tabbas se yanxu yake zargin akwai abinda daddy yaboyemasa gameda inda yakai ilham

to amma shiyasan duk inda ilham take dole zata so haduwa da yar uwarta watarana danhaka dolene yaje yadauko ameera aduk inda take afadin duniyarnan yakawota gidansu Dan yasan dole ilham tadawo gareshi

text yayiwa moneer private  yace mishi yaturo mishi address nasu dakuma phone number dinshi

moneer Wanda dama zaman jiran reply dinshi suke be bata lokaciba yamishi sending abinda yabukata

koda zuwan sakon wayar Anwar mikewa kawai yayi yashiga toilet yayi wanka yashirya cikin shigar alfarma wayarshi yadauka bayan yadebi kudi masu yawa

excode dinshi yakira awaya akan sushirya gashinan fitowa zashi anguwa su kansu excode din seda sukayi mamaki dan rabonshi da fita anguwa kusan shekara guda kenan Dan haka cikin sauri suka shirya komai yana fitowa suka budemishi mota yashiga basu zarce ko inaba se airport yana zuwa jirgi is ready dayake jirgin na shugaban kasane Kai tsaye  wayarshi yaciro yakira gomnan Kano yashaida mishi yana zuwa nanda 40 minutes

[2/11, 12:55] Zahra muhd mahmud□: *ALLAH GATAN BAWA*□□□□□□□□□□

Zahra Muhammad mahmud

*page 57-58*

Suna isa Kano motocine birjik na Security da gwamna yatanadar masa Kai tsaye yabasu umarnin sukaishi wudil gidan me gari

Se alokacin yakira moneer yashaida mishi gashinan zuwa garin dan tuni ya iso Kano ba moneer ba harsu megari seda zuwanshi yabasu mamaki

Sunanan zaune suka fara jiyo jiniya takoina acikin garin hakanne yabasu tabbacin ya iso

Hankalin yan garinne yatashi sabida jin jiniyar alhalin sunsan bakasafai masu mulki suke zuwa garinsuba

Akofar gidan megarin motocin suka faka Wanda tuni megari da moneer sunfito domin tararsa iso suka masa zuwa cikin gidan adakin megari suka saukeshi yayin da security nsa suke jiransa akofar gida

Bayan gaisuwa aka gabatarmasa da abinci

Amma anwar ko kallon abincin beyiba illa tambayarsu ina ameeran take dasauri megari yakirata

Shigowa tayi jiki asanyaye tasamu guri tazauna sannan tagaisheshi

Yaamsa fuska cike da walwala danji yakeyi kamar yaga ilham

Tambayarta yashiga Yi dangane da aynihin tarihinsu kuma yabukaci data sanar dashi gaskiya

Batare data boye mishi komaiba tasanardashi tarihinsu seda kwalla tazubo a idon anwar ashe spouse dinsa marainiyace yadunga azabtar da ita kuma yayi imani batasan iyayentasun rasu ba share hawayensa yayi sannan yayiwa ameera taaziyya

Sumasu megari duk sunmasa bayani agame da abunda suka sani akansu ameera

Besheda musu halin dayake ciki ba na rashin ilham

Illa kawai yanemi izinin megari nason yatafi da ameera Abuja sabida komai dare yau ze wuce

Megari beji dadin rabuwa da ameera ba amma bashida yadda zeyi shiyasa yaamince

Anwar ne yafahinci megarin ranshi besoba shiyasa yace wata guda kawai zatayi tadawo kayi hkr

Special number dinsa yabasu Wanda in akira Kai tsaye zaa sameshi sannan yamike domin tafiya bayan yaajiyewa megari kudi wanda suke dollars ne Wanda shikanshi besan adadinsuba megari kusan suma yayi azaune sabida ganin yawan kudin Wanda tunda uwarsa ta haifeshi betaba ganiba😀

kofar gida yawuce yayin da ameera tashiga hada kayanta bata bata lokaciba tagama Hadawa tayi sallama da matan gidan tanata kuka

Moneer ma dakyar sukayi sallama dayar wayarshi yadauko Yabata sannan yace zasu dunga waya kuma kafin tadawo zezo yasameta ahaka suka rabu taje tasamu Anwar dayan bangaren yasa aka budemata tashiga suka dau hanya tana ta kukan rabuwa da gidan megari dan tanaji ajikinta kamar tabar gidan kenan har abada ahaka suka dau hanyar Kano

Kai tsaye gidan gomna suka wuce bayan gaisuwa tsakanin anwar da gwamna

se gwamna yake cemishi tun dazu akace ka iso amma najika shuru murmushi yayi sannan yace wlh dady wani uzuri ne yakawoni me muhimmanci kuma harna kammala yanzu haka Abuja zankoma

sekace ana korarka anwar inji gwamna

murmushi yasakeyi sannan yace bahakabane daddy

Amin afuwa zan wuce yanxu

gwamna beso anwar yatafi ba amma bashida yadda zeyi yahanasa Dan yaso ace su gana da nafeesa kozeji tausayinta

har airport gwamna yarakoshi se anan yaga ameera yayi zaton ilham ce Dan Tsananin kamarsu yace amma anwar baka da Kirkikazo da iyalinnaka amma baka kawota mugaisaba murmushi yayi sannan yakalli shashin da ameera take wacce tayi firifiri sabida rashin sabo sannan yace daddy wannan ba ilham bace kanwartace

murmushi gwamna yayi Dan se alokacin yalura ilham tafi wannan kilewa sannan yalura wannan Kamar akwai duhun Kai atattare daita

sallama suka  masa suka shiga jirgi suka daga zuwa abuja Wanda ameera jitake kamar zata sume sabida tsoro yayinda azuciyarta godiya takewa Allah sabida adalilin yaruwarta you tayi ido biyu da gwamna Wanda da sede taganshi a hoto ko TV nabiyu gata ga Dan shugaban kasa duk adalilin ilham nakarshen shine yafi mata dadi wato jirgin datashiga godiya tasake yiwa Allah yayin da dokin ganin ilham da yaranta yacika zuciyarta

*10:00pm*

suka isa gida bayan andaukosu daga airport kaitsaye part din su mommy yawuce da ita

suna zaune dukansu afalon suna jimamin me anwar yajeyi a kano sabida lokacin daya fita basanan security nsane suke shaidamusu sunkaishi airport yatafi Kano

sallamarshi ce takatsemusu hirar

ganin wacce kebinshi abayane  yasasu hada baki gurin kiran sunanta

ilham!!!!

harda daddy ba itabace yabasu amsa se alokacin suka kureta da ido sannan suka gane ba itabace kamace kawai bama kamar daddy da mommy sabida sunsan ilham tadade dawuce wannan matsayin

ameera zubewa tayi akasa jiki nabari wai yau itace gaban shugaban kasa da matarsa lalle iko se Allah

gaishesu tayi sannan duka suka sami guri suka zauna

daddy ne yafara mgn tabbas Anwar duk daga inda wannan take tahada jini da ilham Diyata Dan haka kuyi saurin sanar Dani wacece ita

anwar umartar ameera yayi data sake basu labarinta

batare da bata lokaciba tasake basu tunda tafara bada lbrn babu Wanda beyi kukaba afalon harda daddy sabida tausayinsu

ihsan ce taje tarungume ameera Tana kuka kamin daga baya mommy tabi bayanta dadyne yaci gaba da mgn

kallonsa yamaida kan Anwar sannan yacigaba

anwar matarka ilham Tana kasar London kuma sati mezuwa zata dawo Nigeria iyaabinda zan shaida maka kenan game da matarka

dagudu anwar yamike yaje yarungume daddy yanamasa kiss afuska fadi yakeyi thanks you daddy  ngd da wannan albisheer dakamin daddy ne yakatseshi nafada makane badan komaiba sedan ameera sabida nasan zata bukaci ganin yar uwarta kaga dole inmata bayani inda take

amma wlh dabadan hakanba se in tadawo zaka ganta

shide godiya yacigaba dayi

ihsan daddy yama umarnin takai ameera dakinta tashi tayi taja trolley din ameera sannan tarike mata hannu suka wuce

anwar ne yasake yiwa su daddy bayanin yadda akayi yasamo ameera  mamaki sukayi daga baya suka jinjinawa social media

daddy da mommy ne suka wuce dakinsu yayin da anwar shima yawuce nasa part din farin ciki duk yabi ya isheshi jiyake kamar yabita London Dan yakosa satin yacika yadawo abar kaunarsa

abangaren ilham zuwa yanxu takammala karatunta se shirin dawowa gida takeyi murna duk sukeyi ita da inna su twince ko zuwa yanxu sun iya fadin mommy da daddy dan wayone dasu (kamar yusuf dina)

yaune doctor Adnan yasanar da daddy nsa labarin ilham danhaka be bata lokaciba yace yakaishi yaganta dayake daddy yazo London din Kuma shima Adnan yazo

kaitsaye gidan su ilham suka je koda daddy yaga ilham jikinshine yafara rawa daauri  Adnan yazaunar dashi itama ilham Tana ganinshi ta tuno da mahaifinta dagudu taje tarungumeshi tana cewa abba Dan ita azatonta mahaifintane dakyar inna ta banbareta ajikinshi sannan dukansu suka zauna tambayar inna daddy yayi game da alakarta da ilham bata boye mishi kmaiba tafadamishi

dubansa yakai ga ilham wacce har yanzu Tana rike da hannunsa ta kwantar da kanta akan kafarsa

tambayarta yajuya zeyi Adnan yakatseshi

daddy ko katambayeta baabinda zata iya sanar dakai sabida yawancin abubuwa tamantasu inaga kahakura har zuwa lokacin dazata koma Nigeria semu bisu Dan musamu Karin bayani

idon daddy ne yasauka akan sarkar dake daure awuyan ilham dasauri yakai hannunsa kan kwadon sarkar yana dubawa

wlh wannan kodaga ina take jinin Dan uwanace ita shine abinda yafito abakin daddy sannan yacigaba sabida wannan sarkar tamahaifiyarmuce iri biyu gareta tabani daya taba Dan uwana daya tace inmuka haifi yaya mata semu basu Dan haka tabbas wannan jininace innane yadaure dan haka Adnan yabasu shawarar abar maganar zuwa dawowarsu Nigeria shine zasu sami Karin bayani amma anan babu abinda zasu gane hakan akayi domin dukansu sun amince da shawarar da  Adnan yakawo

su twince ne suka shigo falon suna gujegujensu idon daddy ne yasauka akansu dasauri yadaukesu yadora acinyarsa tabbas dayake basu da kwuiya wasansu suka cigaba dayi cikin wasanne sukayi arba da gemun daddy habawa ay basu Yi sanyaba suka shiga Dan sundauka wani nauin kayan wasanne

love you all  maman yusuf

[2/13, 23:15] Zahra muhd mahmud□: *ALLAH GATAN BAWA*□□□□□□□□□□

Salam masoyana  kuyimin afuwa asakamakon rashin jina dakukayi nagode

*page 59-60*

*RANA BATA KARYA*

Tun kafin jirgin su ilham ya iso airport tuni su daddy sunzo tararsu

Ko ina inka Kai dubanka  yan jarida ne suna jiran isowar jirgin

Anwar kuwa ji yake kamar yatashi sama yataro jirgin

Basu jimaba jirgin yasauka dauke da ilham da twince dinta da Inna da Adnan da Abban Adnan

Su twince ne  suka fara saukowa wohoho jamaa naso ace kuna gurin yayinda ilham tabiyo bayansu shigace ta alfarma ajikinta fuskarta sanye cikin bakin glass kayan jikinta Jane da green Swiss less sauran kwalliya nabarwa masu karatu kuyi mata da kanku

Anwar numfashinshine yadauke yayinda yake tunanin Anya wannan ilham ce kuwa tunaninshine yakatse lokacin da daddy yataboshi yana cemishi to anwar gafa ilham kobaka ganetabane kallon daddy yakeyi kamar wani wawa dan tuni yagama raina kansa dan koda hadi ilham tawuce tunaninsa

Ameera ma tagane ilham but tana mamakin yadda ilham din tacanja one time haka binta kawai takeyi da kallo

Itako ihsan dama harga Allah bata ganetaba

Babu abinda yakara firgita anwar seda ilham tafara takowa zuwa gurinsu ganin yadda hips dinda ke rawa cikin wani yanayi tafiya take kamar tarwada yayin da su twins suka rugo da gudu suka rungume daddy domin sun ganeshi

Mommy ce takarasa ta taryo ilham yayin da yan jarida suka fara aykinsu tamvaya suka shiga Jerawa mommy agame da farin cikin datake ciki sakamakon dawowar surukar tata

Dariya mommy tayi sannan tayi godiya ga Allah daya dawo da ita Lfy

Juyawa sukayi kan ilham inda tashiga bayani cikin harshen turanci wayyo duniya 76 76naso ace kunga irin firgitar da anwar yayi dayaji zazzakar muryarta hmm abin baacewa komai

godiya tayi ga Allah sannan tagodewa daddy da mommy da inna

Dakyar suka barsu suka karaso gurin daddy  shima seda security suka dakatar dasu

Idon ilham ne yasauka kan anwar gavantane yafadi ganin kamannin dayakeyi da twins Wanda ko baa fada mataba tagane shine mahaifinsu

tsananin kiyayyarsace  taziyarci zuciyarta Dan ita da Tana da hankali lokacin da zaa auramatashi bazata yardaba sabida har ga Allah bata kaunarsa tsarinshi Sam beyimata ba amatsayin miji tofa!!!

Tana cikin wannan tunanin ne taji anrungumeta dasauri takai dubanta gurin ameerace kuma tabbas taganeta sabida jini daya bawasa bane  ita ma rungumeta tayi Tana kiran sunanta tambayarta tashiga Yi ina mahaifansu kukan ameerane yakaru ganin hakane yasa daddy yace sushiga mota suwuce gida dasauri aka budemusu motoci sukai tashiga

Wanda se alokacin daddy yasamu damar gaisawa da amininsa wato daddyn Adnan Wanda shi tunda yaga ameera yakara rikecewa

Anwar yana zaune ne kurum Dan gama yagama firgita da kallon da ilham take masa Wanda yayi imani kallon kiyayyane wasu zafafan hawayene suka zubo masa na danasani 😭gashi su twince dinsa ko kallo be ishesuba kaichonshi

koda suka isa gida gabadaya part din daddy suka nufa abinci sukaci Wanda har yanzu ilham  na makale da ameera  yayin da shikuma anwar yasamu damar daukar twins dinsa basumishi kiwa ba sabida bahalinsubane sonsune ke Kara shiga zuciyarsa yana danasanin wulakanta  mahaifiyarsu

falo suka dawo gaba dayansu domin daddyn Adnan yace yanada mgn

farawa yayi da basu tarihin bacewar Dan uwansa har zuwa sanda Adnan yahadashi da ilham a London

kuma yanzu bayan yazo Nigeria kuma seyaga ameera Dan hakan  yana bukatar Karin haske

daddy ne yafara bashi lbr iyakar abinda yasani sannan itama ameera tafadi Nata

tun bayan rabuwarsu da ilham har zuwa yanzu

ilham yanke jiki tayi tafadi kasa sumammiya dagudu anwar yayo kanta yanakiran sunanta

ruwa ameera ta dauko aka yayyafamata koda tafarka wani kuka takeyi metsuma zuciya  Wanda har yanzu Tana jikin anwar dago kanta tayi taganta ajikinshi dasauri takwace kanta

daddyn Anwar ma kuka yakeyi Kamar yaro yayinda kowa na falon seda yatayasu

dakyar akasamu duka sukayi shuru yayinda Alh Imam yayiwa daddy godiya abisa nemawa ilham magani dayayi Adnan ma godiya yataya daddy nsa

alfarma yanema agurin anwar da daddy akan yanaso yatafi dasu ilham gidansa Dan yanaso yakaisu meduguri suka ragowar danginsu daya gano bayan komai yalafa

daddy yaamince batare da damuwaba yayinda anwar beso hakaba amma bashida zabi tunda daddy yagama mgn

washe Gari dasafe suka dau hanyar kaduna yayinda har yanzu ilham kukan mutuwar iyayenta takeyi  Adnan ne ke rarrashinta yana bata baki dangama daddy yagaza mgn Don shima kukan yakeyi  ahaka har suka isa kaduna yayinda su twince se tsalle tsallensu sukeyi ajikin daddy

maman yusuf

[2/14, 20:49] Zahra muhd mahmud□: *ALLAH GATAN BAWA*□□□□□□□□□□

Zahra Muhammad mahmud

*Page 61-62*

Suna isa gida momyn Adnan kamar zata cinyesu se rungumesu takeyi basuba basu twins ba

Bayan sunci abinci kowa wanka yayi yayi sallah yabi lafiyar katifa

Shakuwace me tsanani tashiga tsakaninsu dukansu mutanan gidan ilham ko da ameera kamar zasu maida junansu ciki sabida tattalin juna yayinda kullum ameera namakale da waya tana waya da moneer soyayyace sukeyi bata wasaba abun har mamaki yakeba ilham sabida gani take gaba daya ma nawa ameera take

Satinsu guda akaduna suka daga zuwa meduguri

Sunga tarba agurin danginsukowa jiyake dasu se godiya akewa Allah da ganinnasu yayin da aketayiwa iyayensu addua

Sosai suke samun kulawa agurin danginsu allabasshi su twins iyayen farin jini

Satinsu biyu suka koma kaduna bayan komawarsune

Daddy yace ilham tashirya ta koma gidan mijinta kuka tarushe mishi dashi akan ita don Allah yamata rai yakyaleta itafa batason anwar kokadan azuciyarta

Kan daddy ne yashiga charge sabida jiya sukayi waya da daddyn anwar yashaida mishi jibi ilham zata dawo amma yanzu ga abinda ilham take fadi dankari

Kasa yayi da muryarshi ta sigar rarrashi yafara bata baki akan tayi hkr takoma

Itako ilham ina ko sauraronshi batayi sabida kukan datakeyi mommyn Adnan ce tasa baki akan daddy yakyale ilham yanzu ita zata mata mgn

hakan akayi kuwa domin mommy har daki tasamu ilham tafara rarrashinta gami da nuna mata illar dake cikin rabuwar aure inda hartake cemata yanzu inkinki kikoma dakinki mijinki aure zeyi Sannanyazo ya amshi yaransa ahannunki yaba matarsa itakuma inba ta Allah bace azabtardasu zatayi kinfison yaranki sutashi suga iyayensu basa tare kinasone yaranki su tashi cikin rashin syy mahaifiyarsu kiyi tunani ilham nibanga laifin anwar ba yakai matsayin dayakamata kowacce mace tasoshi ko wani laifin yamiki ne dasauri tadaga kanta sannan tace tunda aka fita dani waje betaba zuwa inda Mukeba ko awaya betaba kiranmuba har zuwa nasamu Lfy ko murna betayani

murmushi mommy tayi sannan tace kimasa uzuri sabida bakisan meya hanashi zuwaba

Dakyar mommy tashawo kan ilham tayarda zata koma sabida yaranta amma tayi alwashin anwar se ya gwammace mutuwa akan zama da ita😷

*ABUJA*

mommy da ameerane suka dawo da ilham dakinta a falon mommy suka sauka su twins naganin mommy suka je gurinta da gudunsu suna dariya waisu sunganeta

Anwar ne yashigo da sallamarsa fuskarsa dauke da faraa gaida su mommy yayi yayin da yakai dubansa kan gimbiyarsa akayi ko saa suka hada ido wata uwar harara ta wurga masayayinda shiko jikinshine yakama rawa dangama harga Allah yanxu yana shakkar ilham Dan kwarjini take masa baya iya jure kallonta ballantana yanzu data wurga masa harara  guri yasamu yazauna

Bajimawa daddy yashigo nanma gaisuwa akai tayi tsakaninshi dasu ilham

naseeha sosai daddy yamusu yayinda daddy yakara Jan kunnan anwar akan takiyaye kar yakuma maimaita abinda yafaru tsakaninshi da ilham ita kuma hkr daddy yasake bata akan abinda anwar yamata

kan ilham ne yadaure Tana tambayar kanta me anwar yamata abaya har ake sake jamishi kunne ita kuma ake bata hkr shuru tayi Tana tunani tabbas akwai abinda Yamata kuma tasha alwashin seta binciko ko menene

mommy da ameera ne sukace ta tashi suje da ita part dinta in Dan sunaso su wuce da wuri dan daddy yace karsu kwana mikewa tayi jiki ba kwari Tama su daddy sallama tabisu  suka nufi part dinnata Wanda rabonta dashi tun ranar daaka kawota

komai nanan fes kamar yanzu akasakasu sede yanzu hotunan su twince ne takoina agidan

fada sosai mommy tasake yimata inda daga karshe sukamata sallama suka wuce kuka takeyi sosai yayinda ameera ketayata ahaka suka tafi suka barta part din su daddy suka koma sukayimusu sallama yayinda daddy yabada excode mota goma su rakasu gida

gadiya suka musu sosai sannan suka dauki hanyar kaduna

anwar yana ganin sun tafi mikewa yayi Yamasu mommy sallama yanufi partydinsu hannunshi rike dasu twins yayinda zuciyarshi keta bugawa kamar zata fito addua kawai yakeyi akan Allah yasa hukuncin da ilham zata masa yazamo me saukine agareshi gashi inna ladi tun bayan tafiyarsu ilham kaduna itama tawuce gida dan taga yan uwanta da seyaje gareta yayi kamun kafa kozata shawo masa kan gimbiyar mata wato ilham

itako ilham tun dasu ameera suka wuce wanka tashiga tayi yayinda tsantsara kwalliya afuskarta kamar me shirin zuwa party

wasu arnayen English wears tasaka rigar bata rufe mata cibiyaba yayinda daga saman rigar nonuwanta Duksunfito gasu Masha Allah

daga bayan rigar kuma wasu igiyoyine akayimusu style kamar yadda ake daure igiyar kambus

rigar maroon color ce yayinda wandon shikuma fari ne jeans kuma irin pensur dinnanne amma kuma duk an yayyagahi alamun kwalliyarnan da ake cewa crazy jeans

gashinta sakinshi tayi a gadon bayanta tura ruka tashiga pesawa kamar bagobe dama gashi dataje meduguri tasiyo wasu masu kyau

falo tadawo tazauna tadora kafa daya kan daya Tana dan girgizasu yayinda bakinta kuma tana taunar ciwingum agaskiya bakarya ilham tahadu musamman rigar jikinta bame hannu bace shine yakara fito mata kyanta abunka da farar mace iya kyau ilham tayi kyau ba namijiba ko mace kika Kalli ilham alokacin sekin maimaita to inaga anwar Kuma

jiran shigowar anwar kawai takeyi

shiko yana waje yana ta adduoi Akan Allah yataimakeshi

to masu karatu gade ilham tayi kwalliya tadaukar hankali waito hakan na nufin Anwar tayiwa kwalliyar Dan yaji dadine ko kuwa

maman yusuf

[2/15, 16:25] Zahra muhd mahmud□: *ALLAH GATAN BAWA*□□□□□□□□□□

Zahra Muhammad mahmud

*Page 63-64*

Tura kofar anwar yayi yashiga jiki asanyaye bata falon kasa Dan haka Kai tsaye yahaura sama

Gabanshine yafadi saura kadan ya yarda su twins dake hannunshi

Sabida arba dayayi da ilham Cikin shigar da ko amafarki bezaci zata iyaba

Sauke su twins yayi suka ruga gurin mamansu shikuma yaci gaba da tsayuwa agurin kamar andasashi

Ilham ko se ayko mishi take da sakon harara mikewa tayi taja hannun su twins suka shige daki tafiya take tana juya masa uku Wanda yananyin datake juyasu ko namiji ladifine inyagani seya koka balle anwar cikakken namiji Wanda tuni hankalinsa yakai kololuwa gurin tashi

.binta yayi da kallo harsuka shige daki zama yayi yadafe kansa yana tunanin menene mafita.

Yana zaune agurin har aka Kira sallar magrib

Mikewa yayi yashiga bayi yayi alwala yawuce masallaci

Bedawo gidanba se takwas

koda yashigo suna zaune afalo suna kallo gefenta yaje yazauna ko kallonshi ilham batayiba tamaida hankalinta kan kallo

Mgn yafarayi cikin muryar tausayi da neman gafara

Ilham Don girman Allah ki ajiye duk abinda ke ranki muzauna Lfy wlh nime kaunarmine kitausayamin Don Allah

Tsakine amsar data bashi bata bata lokaciba tanufi dakinta

Dan har ga Allah ita haka kawai anwar bemataba amatsayin miji shiyasa ta tsaneshi sosai

.koda tabar gurin anwar kasa daurewa yayi beyi auneba Kawaiseji yayi hawaye nabin fuskarsa yarasa gane meyasa baya iya daure damuwa daga ilham one time take sashi kuka

Itako ilham tana shiga daki wanka tayi tasauya kayanta dawata arniyar night gown

Turare tafesa akowanne lungu najikinta sannan tafito falo domin daukar su twins nide nace tafito tsokanane

Anwar naganinta zumbur yamike sabida bemasan meyakeyiba

dukawa tayi Wanda hakan yasa har Dan fant din dake jikinta yana hangowa tuni miyaun bakinshi yakafe soyake yayi mgn amma ba kalma abakinnasa duk sun gudu

Ranar kwana yayi wanka da ruwan sanyi sabida muguwar shaawar data taso mishi gashi ba fuska agurin ilham dan kulle dakinta tayi

*Bayan shekara daya*

Zuwa yanzu anwar iya horuwa yahoru agurin ilham gashi abinda yafi bashi takaici tsawon lokacinnan Kala ilham batacedashiba sede yagama bata hakuri ta tashi tabashi guri

Gabadaya yarasa ina zesa kansa koda yakaima su daddy Kara ko kulashi basuyiba bare yasa ran zasu taimaka masa zuwa yanzu jiyake kamar zeyi hauka

gashi yanzu ilham mkrt take zuwa Dan tuni daddy yasamomata admission a Abuja Turkish university

Inda take karantar medicine

su twins. ma tuni ansasu amkrt suna play class shikadai suke bari sutafi

Abubuwa da dama sunfaru aciki harda zuwa nemanwa moneer auran ameera inda daddy yawakilta megari ne yafi cancanta daya aurar daita duk da yanzu bata gidan megari takoma hannun daddy da zama inda ahalin yanzu Tana kasar India Tana Karasa secondary school dinta Adnan tabi shike kula da ita

inda adaya bangaren soyayyace takullu me tsanani tsakanin Adnan da ihsan inda akasa rana auransu dazaran ameera takarasa mkrnt kuma duka family sunyi farinciki da auran

Ilham ce zaune adakinta Tana rage kayan jikinta dawowarta daga makranta kenan

anwar ne yafado daki da sallamarsa

aykinshi Dan kullum yashiga Yi wato bata hkr

ran ilham ne yagama baci Dan haka taga yadace ta taka masa burki

tsawa ta dakamasa tahanyarcewa dalla malam dakata anwar Kake kowa wlh kadami rayuwata tsawon shekara guda kana bani hkr ban hakuraba Kai jakine dabaza ka gane hakurinne bazanyiba

dasauri anwar yakalleta sabida kalmar jaki data kirashi da ita ranshi ne yasoma baci sabida tunda yazo duniya babu wani Mahalukin daya taba cimishi mutunci kamar ita ayau

tunaninshi ne yakatse lokacin dayaji tacigaba da mgn

koda yake ay Kare dama bashida zuciya Dan haka inaso kajini da kyau wlh anwar bana sonka bana kaunarka natsaneka tsanar da ko mutuwata banayiwa ita Kuma wlh bazantaba sonkaba har abada duk ranar dakaji bakina yafurta yana sonka wlh karya nakeyi karka yadda inkokayarda inasonka toko tabbas harka mutu sunanka jaki a idon duniya

tarine yaturnuke anwar tunyanayi atsaye har yadurkusa itako ilham tana gama fada masa mgn tawuce toilet ta kyaleshi

shikuma yaci gaba da tarin yana rike da gefen zuciyarshi zuwacan yafara aman jini mikewa yayi Dan yafita adakin ahankali yafara bin step zuwa kasa ko rabi beyiba ya yanke jiki yafadi yafara gangarowa Wanda hakanne yayi Dede da shigowar ihsan rike dasu twins andawo dasu daga mkrt sakinsu tayi dasauri ta isa gurinshi

aman jini yakeyi sosai juyo dashi tayi abinda taganine yasata kwalla wata gigitacciyar kara kamannin anwar gabadaya Sun sauya maana fuskarsa tadan karkace harda bakinsa ga jini nazuba abakin Wanda ko baa fadamataba tabbas tasan anwar yasamu paralyse😷

maman yusuf

[2/16, 19:38] Zahra muhd mahmud□: *ALLAH GATAN BAWA*□□□□□□□□□□

Zahra Muhammad mahmud

Nagaisheku masoyana baride indan taka□86□86□86□86□86□86□86□86□86□86□86□86

*page 65-66*

Agigice ihsan tajuya da gudu domin kiran mommy

Suko su twins kuka Sukasa sabida ihun ameera yafirgitasu

Kukannasu yayi dede da fitowar ilham daga wanka dasauri tazura doguwar Riga tafito folon dan ganin meyasasu kuka

Tahowa take dasauri danhaka bata lura da anwar dake kwance akasaba seji tayi tayi tuntube da Abu tuni tafara tambul akasa bakinta ne yabugu da center table tuni yafara jini

Dakyar tamike takai dubanta inda taji tuntuben gabantane yafadi ganin mutum akwance dasauri tamike taleka fuskar nakwance ido taware sosai ganin anwar akwance cikin jini gashi halittarshi tasauya

Tunani tafarayi akan to anwar kasheshi akayi tahanya caka masa wuka koko fuskarshi aka watsawa wani abun dayasa ta karkace wani sanyine yaratsa zuciyarta gami da adduar Allah de yasa mutuwa yayi Kai dako naji dadi kalar dadin data tuno zatajine yasata fara taka rawa hartana juyawa harsu

Mommy da ihsan suka shigo agigice batasan sunshigoba se rawarta kawai take takawa

Jin salatin mommy ne yadawo da ita daga tunaninta dasauri tawaiga inda suke kallon tuhuma mommy takemata

Dasauri suka karasa kan anwar ganin halin dayake cikine yasa mommy faduwa kasa sumammiya

ihsan dawani arnen gudu tanufi security din gidan dasauri suka shigo falon lokacin ilham nakan mommy hankalinta atashe nace kuji rashin kunya gurin ilham

Daukarsu security din sukayi gaba daya sukasa amota yayinda ihsan da ilham suka rufamusu baya akabarwa security su twins agida

Wani katafaren asibiti suka nufa Wanda tunkafin su ISO tuni anyi waya asibitin danhaka koda zuwansu ilahirin maaikatan gurin suna waje suna jiran akawosu

kai tsaye emergency akawuce dasu akahana su ilham shiga awaje suka tsaya suda securities dinsu

Tuni akayi waya office din daddy akasanar dashi cewa yazo fa gida balfy yanxu haka suna asibiti

Hankalin daddy ne yatashi matuka yana tunanin meyafaru da family dinsa dawannan tunanin yakaraso asubiti shida makarrabansa

dasu ilham yaci Karo akofar emergency ward

Ihsan dagudu tafada jikin daddy Tana kuka cikin kukantane take fadamasa abinda kefaruwa

jikinshine yafara rawa alamun zefadi dasauri security dinsa yazaunar dashi

doctor ne yafito daga dakin yayinda abayansa wasu nurse ne guda hudu suke gunguro mommy akan gado hannunta daure da drip

agigice sukayi kanta wani daki aka kaita na musamman

bayan ankwantar da ita doctor yafarayiwa daddy bayanin abinda ke faruwa

Dan durkusawa yayi sannan yafara mgn Kamar haKa

ranka yadade madam bawani abubane yasameta illa frgita datayi  asakamakon ganin abinda yafirgitata wanda insha Allahu nanda wasu lokuta zata farka  dan tuni mukashawao kan matsalar

shikuma yallabai anwar am sorry to say

to say what!!!! Inji daddy

afirgice doctor yace

am Sorry sir but anwar yana cikin halin mutuwa ko rayuwa domin zuciyarshi takamu da matsanancin ciwa Wanda single mistake zaayi ta buga sannan ahalin yanzu yakamu da ciwon paralyse

gaban dadine yayi mummunar bugawa yayinda ihsan tarushe dawani matsanancin kuka. itako uwar gayya wato ilham wani malalacin murmushi ne yabayyana akan fuskarta Wanda faruwar hakan akan idon mommy Dan tuni tafarka Tana sauraronsu

daddy ne yamike yace doctor yakaishi yaga anwar

karaf mommy tace nima zani dasauri suka waiga suna kallonta Dan basusan ta farkaba

daddy ne yaje yarungumeta yayinda itakuma tafashe da matsanancin kuka ihsan ma rungume mommy tayi Tana kuka doctor ne yacirewa mommy drip din hannunta yayin dasu daddy suka matsa Dan doctor yadubata

bayan yagama dubatane tayi yunkurin tashi dasauri ilham takai Hannu domin taimakamata hannu mommy tadaga mata alamar tabarshi  ihsan ce taruko mommy ta Mike abun yadaurewa daddy Kai ammayayi shuru mikewa sukayi suka nufi dakin da anwar yake ga mamakin daddy seyaga ilham tanemi kujera tazauna hankalinta kwance

mamakine sosai ya bayyana afuskar daddy koda ilham tawaigo taga yana kallonta dauke kanta tayi  yana kallonta har yakarasa fita

duk dauriyar daddy dayaga yadda anwar yakoma seda yafashe da kuka kamar yaro su mommy da ihsan ma kukan sukeyi

sefito dasu akayi adakin Dan baason hayaniya agurin dayake

koda suka dawo dakin da ilham take ga mamkinsu waya takeyi da ameera se dariya takeyi bamecewa a asibiti take kuma mijintane Mara lfy

ganinsune yasa tayi sallama da ameera tayimusu sannu da zuwa

daddy ne yaamsa amna kan ihsan da mommy ko kallo bata ishesuba

.suna asibitin har zuwa dare sewajen karfe goma sha biyu nadare suka wuce gida harda mommy sabida asibitin baa jinya

*bayan wata biyu*

anwar yanzu har yanzu anwar ciwo se abinda yakaru babu wani sauki

itako ilham tunda taje asibiti so daya bata sake komawaba amma kullum setayi kwalliya ta tafi mkrt

abun yanama su daddy ciwo sosai babuma kamar mommy wacce tafi kowa jin haushin ilham din amma sabida rashin kunya irinta ilham kullum setaje take gaishesu

su ameera dasu Adnan da daddy nsa da mommy sa dasu megari da yan gidansu moneer kowa yaje duba anwar yafi akirga

koda daddyn Adnan yatamvayi ilham Tana zuwa gaida mijinta kuwa  budar bakinta secewa tayi  aa ita meze kaita gurin Wanda bataso  dauketa daddy yayi da Mari ze karamatane mommy nadnan tarikeshi

fada yashigayi ta inda yashiga batanan yake fitaba daga karshe yace duk sanda bataje ta dubosaba bashi babu ita abinda daddy besaniba tuni daddydaddyn anwar yagama shirin fita da dansa kasar Egypt domin aduba lfyrsa adaren ranar

ayko hakan akayi adaren ranar jirgi yadaga da anwar da mommy da ihsan da daddy zuwa kasar Egypt

se awaya daddy yake shaidawa daddyn Adnan fatan alkhairi yamusu gami da cewa next week sunanan zuwa suma

itako ilham batasan basa nan ba seda taje gaishesu security dake gadin kofar shiga part din yake sheda mata abinda ke faruwa

bataji dadin abinda sukayimataba narashin yimata sallama  jiki bakwari takoma part dinta inda su twins suke ta waansu

kwanciya tayi tashiga tunani gaskia tasan bata kyautawa su daddy ba  batayimusu adalciba sabida basu cancanci haka agurintaba  to amna yataiya dansune bataso kuka tafashe dashi afili tanayiwa anwar Allah yaisa Dan dashi badansu mommy bane baabinda zeshiga tsakaninta dasu narashin kyautawa

kuka tayi me isarta sannan tamike tanufi daya daga cikin dakunan part dinta Wanda bata taba shigarshiba tsawon zamanta agidan koda shigarta dakin kamshin turaren anwar yakeyi jin kamshinne yasa zata juya da sauri idontane yasauka akan wani littafi akan side drower na gadon dasauri taje tadauki littafin haka kawai taji tanason karanta abinda keciki Dan ta Lura diary ne

fara karantawa tayi

abinda tagani a littafinne yarura tsananin kiyayyar da takewa anwar azuciyarta domin kuwa  gaba daya labarin haduwarshi da itane a littafin harda irin azabar daya dunga ganamata hawayene yake zuba afuskarta jin first night dinta a toilet sukayishi bakincikine yaziyarci zuciyarta  tabbas tayarda anwar ba masoyintabane duk da a diary din yafadi irin tsantsan kaunar dayake mata amma bata Lura dashiba kiyayyar daya bayyana yamata itace tafi tsayamata arai daukar littafin tayi ta tafi dashi dakinta yayinda taci gaba da kuka akan rashin kyautawar datayiwa su daddy

Daga karshe yanke shawara tayi akan gobe zata bar musu gida sabida zamanta da anwar yakare Ashe shidin bakin azzalumine haba no wonder taji tatsaneshi da yawa

maman yusuf

[2/17, 21:39] Zahra muhd mahmud□: *ALLAH GATAN BAWA*□□□□□□□□□□

Zahra Muhammad mahmud

*page67-68*

Tun karfe takwas nasafe ilham tagama shiryawa tashirya su twins tadebi kayan sawarsu da duk wani Abu me amfani takira security yafitar mata dasu zuwa mota itama fitowa tayi rike dasu twins suna ganin tafito suka bude mata kofar baya tashige ita dasu twins Kai tsaye kaduna tanufa

Se sha biyu na rana suka isa kaduna

Sallama tayi tashiga falom gidan yayin excode dinta suka shigo mata da kayanta sallamarsu tayi suka juya Abuja

Mommy tunda tashigo take kallonta baki bude

Guri ilham tasamu tazauna sannan tagaida mommy

Bata amsa gaisuwarba tashiga jero mata tambaya

Ilham mekikeyi a nigeria bayan anwar bashida Lfy yana Egypt zaman mekikeyi baki bisu kuntafiba

Baki ta turo sannan tace ni  ni  ni bansan suntafiba ay

Salati mommy tayi tasanar da ubangiji

Sannan tace ilham Anya kinada imani kuwa dama Ashe baki janye wannan maganar tsakaninki da anwar innalillahi wainna ilaihir rajiuna ilham tafadi da karfi

sannan taci gaba wlh ilham kingama asara duniya da lahira yanzu irin wannan sakayyarce tadace da mahaifan yaronnan yau ko yau ko yankaki anwar yakeyi ki mutu ki dawo bedace da abinda kike masa ba

Wlh ko rantsuwa nayi bazan Yi kaffaraba ciwon anwar da hannunki aciki

Tunda baki da hankali duniya zata koyamiki

Kina da yara dashi Amman kike neman kashemusu mahaifi wlh insukayi wayo suka fahimci kece silar mutuwar mahaifinsu ko kallonki bazasuyiba

tunda haka kika zabawa kanki kije kiyi Allah yabaki saa

mommy nagama fadin haka tatashi taja hannun su twins suka shige daki suka bar ilham zaune afalo kamar mayya

Hawaye takeyi kamar fanfo tabbas jikinta yayi sanyi dajin kalaman mommy kuma tayarda tayi kuskure sosai su daddy basu can canci hakaba kuka takeyi kamar ranta ze fita

Gashi yanzu su daddy sunyi fushi da ita uwa uba ga hakkin mijinta har ga Allah yanzu tausayin anwar yakamata tuno irin wulakancin data dunga yimasa yana hakuri tayi wani sabon kukanne yasake kamata lalle tayarda in anwar yamutu itace takasheshi Allah kagafartamin tafadi afili

Babu abinda inta tunoshi yakemata ciwo ayanzu irin yadda mommy taganta Tana rawa alokacin da anwar yafadi ya ilahi cigaba tayi da kukanta harsu mommy da daddyn Adnan suka shigo falon batasaniba seda daddy yayi gyaran murya sannan tadago dasauri

Tana ganinnshi dagudu taje tarungumeshi Tana kuka Tana cewa daddy karkace komai wlh nagane kuskurena kugafarceni wlh bazan Kara ba natuba kakira daddyn anwar kace suyafemin wlh bazan kumaba nayi nadama kukan datakeyine yasa jikin daddy yin sanyi rungumeta shima yayi sannan yace to yaisa haka naji share hawayenki  kuma naji dadi dakika gane kuskurenki dawuri sede fatan Allah yasa agurin mijinnaki baki makaraba Dan iyayensa nasansu zasu yafemiki kitayin addua

haka suka sata agaba sunatayimata nasiha Wanda bakaramin shigarta tayiba

Koda tazo bacci kasayitayi tunanin anwar kawai takeyi da irin cin kashin da tamasa

takosa tasashi a idonta kozata samu sassauci  azuciyarta danjitakeyi kamar zuciyarta zata fashe  haka takwana Tana kuka

*EGYPT*

Tunda suka isa likitoci sunfi goma akan anwar Wanda yake asume suna kokarin ganin numfashinshi yadedeta allurai akayimasa sannan suka daura masa drip daga karshe suka turashi cikin wani machine Dan yataimaka Wajansashi yafarfado dansu sami damar gudanar da aykinsu

gidan dasuka sauka su daddy suka koma sabida baa zama a asibitin

tunda suka shiga gida ihsan da mommy suke kuka dakyar daddy yashawo kansu sukayi shuru wanda koshi kanshi dabasa gurin kukan zeyi Dan dauriya kawai yakeyi

hirar rashin hallaccin ilham sukeyi mommy tace wlh alhaji bantaba tsammanin ilham ko wuta mukace tashiga zata musamanaba amma wai kirikiri tanuna bata kaunar gudan jininmu tabbas ilham tacika tsintacciyar mage kuma tabani mamaki

daddy ne yakatseta dacewa ku kwantar da hankalinku ilham baita tadorawa anwar ciwoba kuma baitace zata yayemasa ba se Allahn daya dora masa Dan haka banaso kuna damun kanku kawai muyiwa anwar addua shine mafita

koda dare yayi basu rintsaba sallah sukai tayi tanafila dannemawa anwar sauki agurin Allah.

koda gari yawaye suka nufi asibitin

babban likitanne yataresu

bayan sungaisane yake shaidamusu anwar yafarka

murna ce takamasu gabadaya suka rungume juna

likitan yaci gaba dacewa tun karfe uku nadare yatashi amma tunda yafarka yanata kiran sunan ilham har zuwa wayewar garinnan duk da maganarshi bata fita sosai asakamakon  paralyse din daya samu

pls wacece ilham dinnan

kallonkallon suka shiga yiwa juna cande daddy yace matarsace

good inji likitan sannan yadora dacewa to magana tagaskiya danku yana matukar kaunar wannan ilham din kuma rashinta akusa dashi ze iya jawowa arasa Ransa

agigice suka Kalli juna

likita yaci gaba

azahirin gaskiya inda hali kukawomasa ita kusadashi

sabida semun samu natsuwar zuciyarsa sannan mudorashi akan magani  zuciyarsa ta kumbura sosai dole da ita zamu fara sannan muzo kan paralyse din dayayi

mommy ce tace zamu iya ganinsa

eh xaku iyamana amma banda yin abinda zebatamasa rai

Jagora yamusu zuwa dakin da anwar yake

idonshi biyu

sunashiga yana kallonsu dasauri mommy taje tarungumeshi kuka yake abin tausayi yanacewa mommy ilham bata sona tace bazata taba sonaba har abada yafadi cikin muryarsa irin tamasu paralyse

Kara rikeshi mommy tayi Tana shafa kansa tace kayi hakuri my son ilham zata soka amma sekayi hkr kakwantar da hankalinka

rokonsu yashigayi akan Dan Allah sucema ilham tayafe mishi koda ta Allah takasance agareshi

maganarshi tafadarmusu da gaba danhaka dasauri daddy yakira daddyn Adnan awaya yake shaidamishi halin daake ciki  hankalinshi atashe

shima daddn Adnan hankalinshi ne yatashi  kwantarma da daddy hankali yashigayi inda yamasa alkawarin insha allahu duk yadda zeyi yasamarma ilham visa itadasu twins yau zeyi zuwa gobe insha Allahu zata iso sallama sukayi yanata masa godiya

doctor ne yashigo yace sufito haka daga dakin hakanan badan ransu yasoba suka tafi gida kowa zuciyarshi namasa zafi

Koda labarin zuwa gurin anwar yasamu ilham ranar kasa bacci tayi dan tun yamma tahada musu kayansu  dan takosa gari yawaye taje tanemi gafarar mijinta. Duk da tasan batasonshi amma Tana tausayinshi yanzu kuma tayi alkawarin zama dashi abatasonshidin

*washe gari*

damisalin karfe goma nasafe jirgin su ilham yadaga zuwa kasar Egypt

anan semuce fata nagari anwar da ilham

maman yusuf

[2/18, 11:56] Zahra muhd mahmud□: *ALLAH GATAN BAWA*□□□□□□□□□□

zahra Muhammad mahmud

*page 69-70*

Ilham ta isa kasar Egypt Lfy kuma su mommy sunyi murna dazuwannata danbasu taba tsammanin zatazoba rungume mommy ilham tayi tana kuka Tana fadin tagafarceta Don Allah wlh tatuba bazata sakeba kuka take iya karfinta tana nemam gafarar mommy

Wani sanyine yaratsa zuciyar mommy kuma dama ita mommy harga Allah tanason ilham dagota tayi Tana sharemata hawaye tace ya isa haka ilham nayafemiki Allah ya yafemana gabadaya

Kafar daddy taje tarike tana wani sabon kukan tace daddy baku cancanci haka agurinaba nayi kuskure megirma amma Don Allah kugafarceni sharrin shaidanne abinda nayimuku natuba tafada taname tsananta kukanta kanta yadafa yace Allah yamiki albarka ilham mommy ma tayafemiki bare ni nayafemiki duniya da Lahira yafadi yana murmushi

Kara durkusawa tayi tanamusu Godiya

Daganan tamike tanufi ihsan wacce secika take Tana batsewa Dan ita bataso suka yafewa ilham ba Dan laifinta babbane

rungume ihsan ilham tayi Tana neman yafiyarta itama tureta ihsan tayi gamida Jan tsaki tabar gurin tofa ilham binta tayi da kallo yayinda wasu siraran hawaye sukacigaba da zubowa afuskarta jitayi andafata dasauri tadago dantaga waye ihsance rungume Junasukayi suna kuka dakyar su mommy suka rarrashesu

doctor ne yafito yace ilham tabiyoshi bamusu tabishi suka shiga dakin da anwar yake

Suna shiga lokacin idonshi biyu kallon ilham yakeyi yayinda wasu hawaye ke fita a idonsa

Dasauri takarasa inda yake itama Tana kuka zama tayi agefen gadon dayake tadago kanshi  tadora akan cinyarta tana wasa da gashin kanshi

Cikin kuka take cewa anwar kagafarceni natuba wlh bazan sakeba kayimin afuwa nacutar dakai dayawa Wanda baka cancanci hakaba kayafemin

anwar Wanda farinciki tuni yagama lullubeshi kanshi yadaga mata alamar yayafeta nuni yamata datadena kuka

Karar bude kofane yasa su waigawa sutwins ne tare da doctor dagudu suka karasa jikin anwar suna daddy daddy yayinda suka haye jikinshi sunata tsalle tsallensu namurnar ganinsa Dan sundade basu ganshiba

Farincikin da anwar yake ciki bashida iyaka koda doctor ya aunashi bakaramin mamaki yayiba ganin cikin kashi Dari kashi hamsin da biyar na kumburin zuciyar anwar yaragu yayi murna sosai sudaddy ma dasuka sami lbr sunyi murna se sama ilham albarka sukeyi tare da rokonta akan takula da anwar Don Allah

*BAYAN WATA UKU*

zuwa yanzu anwar yasamu sauki sosai tuni zuciyarshi tawarke komai ilham take masa batason ganinshi cikin damuwa ko kadan Dan Adan zaman datayi dashi wani zazzafan sonshi yakamata bata daburin dayawuce tafarantamasa

yanzu abinda yay saura kawai shine tafiyar anwar ta dedeta kuma shima kullum ilham seta rike hannunshi sunfita waje Tana koyamasa

Tuni su daddy suka koma Nigerian suda su twins tunda sukaga yafara samun sauki

daddyn Adnan ma shida iyalinshi harda ameera sunzo duba anwar

Manyan yan siyasa tare da yan kasuwa yawancinsu sunzo dubashi sabida anwar mutumne na mutane uwa uba daddynsa mutumin kirkine

Nafeesat ma diyar gwamnan kano so uku Tana zuwa dubashi Wanda hakan bakaramin bakanta ran ilham yakeyiba yayinda shikuma anwar yakejin dadin hakan

yanzu sede muce anwar Allah yakyauta gaba Dan ahalin yanzu babu me kallonshi yace yatabayin paralyse Dan Gama yawarke sumul tafiyarma tadedeta har wata kiba yayi sabida kulawar dayake samu daga ilham Wanda shi har mamaki take bashi yadda itace kemasa wanka shiryashi bashi abinci abaki dadukkanin wani Abu daya bukata har ga Allah yanajin dadin hakan

*Nigeria*

yaune ilham da anwar suka dawo gida kasa nigeria

dubban jamaane suka cika airport domin tarbarsu aciki harda mahaifinshi da mommy da ihsan dakuma su daddyn Adnan

koda suka fito daga jirgi ilham kusan tsorata tayi daganin mutanen dake gurin harkusan faduwa tayi anwar yatarota dasauri itakuma taratayo hannuwanta akan wuyansa suna kallon juna (tamkar arnav da khushi)

masu hotuna aykinyine yasamesu Dan daukar hotunansu sukashigayi kamar bagobe

suko sunyi nisa basu sanma abinda kefaruwaba dasauri ihsan takarasa gurinsu danta Lura shirin yiwa juna kiss sukeyi gudun abin kunya yasa taje garesu rungumesu tayi gaba daya dasauri suka dawo tunaninsu

gabadaya gurin akasa tafi Raf Raf Raf

suko su daddy kasancewarsu yan Boko hakanma burgesu yayi kuma sunyarda yanzu ilham ta gyaru

Karasowa sukayi gurinsu daddy ay su twins naganin iyayensu dagudu suka kwace daga hannun mommy suka nufesu suma suna ganinsu sukaduka suka daukesu suka rungume

dakyar securities suka janyesu zuwa mota Dan gama yan jaridane kamar zasu cinyesu da tambayoyi

Kai tsaye gida suka nufa

inda daddy yahada wata walima sabida farincikin samun saukin anwar

anci ansha anyi bishasha malamai sunyi adduoi sosai sannan akawatse taron

kowa yagaji gashi dama har anyi sallar ishai danhaka kowa part dinshi yanufa

ilham nashiga dakinta komai nanan pes wanka tayi tayi alwala tayi sallah sannan tazauna gaban madubi ta tsantsara kwalliya Dan yau sotake tafara faranta ran soulmate dinta Sunan databa anwar kenan

wata fitinanniyar rigar bacci tasa base namuku bayaniba atakaicede tahadu

turaruka tashiga fesawa jikinta

sannan tazauna zaman jiran anwar yafito

Dan su twins suna part din mommy

tananan zaune har karfegoma amma anwar befitoba danhaka tanufi dakinshi taga ko lfy

tura kofar tayi taji akulle danhaka tashiga nucking daga ciki yaamsa mata da wai wayene yake damuna😳

jiki asanyaye tace nice yace kewa dankari kirjinta tadafe sabida wani mugun bugawa da zuciyarta tayi nufinshi begane muryartaba daurewa tayi tace ilham

banza yayi da ita takai awa guda atsaye abakin kofar tanajiran koze budemata kofa amma shuru

dakinta takoma tahaye gado Tana kukan takaici meyasa anwar zemata Hakan kode dama be huce bane amma inde yace haka zemata gaskiya ze kwareta sabida yanzu sonshi takeyi kamar ranta

kwalliyar datayi ta goge sannan tacire rigar baccin tasa wata tahaye gado Tana ta kukan tausayin kanta

maman yusuf

[2/18, 18:08] Zahra muhd mahmud□: *ALLAH GATAN BAWA*□□□□□□□□□□

zahra Muhammad mahmud

*Page 71-72*

Ranar ilham batayi bacciba kwana tayi kuka

Shiko abangaren anwar daurewa kawai yayi yawa ilham wulakanci beso ba to amma bashida zabi dole ne yakare martabar sunanshi na anwar a idon duniya

Duk yadda ilham taso su shirya da anwar batasamuba sabida baya bata fuska tayi kuka tayi magiya akan yafada mata abinda tayimasa amsa dayace bakiyimin komai daraja da martabar Sunana na anwar nake karewa a idon duniya

Duk sanda yabata wannan amsar rasa ina zata sa kanta takeyi  sabida kwatakwata takasa gane meyake nufi

Dayake dakanta take girki ko abinci tashirya masa bayaci yadda taajiye haka zata dauki kayanta

Damuwar datake cikine yasa gabadaya tayi duhu tarame  ko abinci bata iya ci kuma bazata iya tunkarar kowa da matsalartaba tabarwa cikinta

Tuni takammala karatunta inda kuma tasamu  results me kyau

Daddy yashiryamata walima haka aka gama taron ba anwar abin bakaramin ciwo yamataba amma ta danne

Mommy ce takirata take tambayarta shinko akwai abinda kedamuntane dayasa tarame haka

Babu komai taba mommy amsa

Kintabvatar inji mommy

Kai Kawai tadagawa mommy

Mommy de takyaletane tunda batason fadamata Amman tabbas tasan akwai abinda kedamunta

Shiko anwar anashi bangaren yanzu soyayya yakeyi da nafeesat yar gidan gwamnan Kano sabida yanzu yayarda da kalmar hausawa dasukace kaso mesonka

nafeesat kuwa jitakeyi Kamar tafi kowacce mace saa aduniya tunda anwar yadawo dasoyayyarsa gareta

Kusan duk Friday yana Kano yaje gurinta soyayya sukeyi kamar zasu cinye junansu

Mahaifinta bakaramin farinciki yayi da hakanba

Anwar yaune yayanke shawarar sanarwa da daddy aje nemamasa auran nafeesa Dan so yake ahada bikin dana su ihsan Wanda yanzu saura wata biyu ayishi

Dan tuni ameera takammala karatun

A Falom daddy yasamesu shida mommy gaishesu yayi sannan yasanar da daddy bukatarshi tason auran nafeesa

Jikin mommy da daddy ne yayi sanyi dajin batun

to amma basuda ikon hanashi abinda yakeso kuma dama Sunsha alwashin bazasu sake tilastamasa yin abinda bayasoba

daddy ne yafara mgn dacewa aurefa kace anwar  Anya kuna zaune Lfy da matarka kuwa

Amsawa yayi dacewa Lfy lau muke zaune kawai de ina raayin aurenne kuma inason nafeesan kuma ko na aureta banan gidan zan ajiyetaba gidana Dana Gama ginawa a asokoroad can zan kaita kunga bamasa guri daya bare har suyi rigima

daddy ne yakatseshi dacewa  wannanne baze yiwuba sede kahadasu guri daya konan gidan kocan gidannaka

alfarma yanema akan to subari yafara tarewa da amaryarsa inyaso daga baya ilham takoma

kin amincewa daddy yayi inda daga karshe yabashi umarni akan ana saura sati daya Bikin yadauki ilham yamaidata gidan tafara zabar inda takeso sabida itace babba amma inyace amaryace zata fara shiga gidan yajawa uwar yayansa raini

amincewa yayi da batun daddyn

mommy cewa tayi to my son Allah yatabvatar da alkhairi sede inason kasani Dan zakayi aure baka isa kawulakanta ilham ba muddin kasan bazakayi adalciba karkasoma inbanda rigima irin taka nawa Kake dahar zakayi mata biyu nide kaji tsoron Allah kawai shine fatana kuma kaje kasanar da matarka

Hakade sukaitamasa nasiha  akan yaji tsoron Allah yayi adalci

Sallama yamusu yawuce part dinsu

afalo yasamu ilham ita dasu twins tana koyamusu homework

dakinshi yashige bayan yama su twins wasa

Ilham ko Kokallo bata isheshiba

*bayan wata guda*

zuwa yanzu anje antambayarwa anwar auran nafeesat kuma antsaida ranar daya datasu ihsan

danhaka nafeesat tamatsamaa akan suje suyi free wedding pictures

ayko haka akayi sunyisu Kala Kala sewanda yagani tuni harsun bazasu a social media kowa se fatan alkhairi akemusu bama kamar nafeesa daake ganin tagama saa

ilham baiwar Allah batasan wainar daake toyawaba

Tana zaune adakinta da daddare anwar yayi sallama yashigo dakin

mamakine sosai akan fuskar ilham naganinsa inda daga karshe farinciki yakamata naganin Allah yaamshi adduarta anwar yazo gareta

tsugunawa tayi tagaisheshi kallonta yayi yaga tarame gawani baki datayi kamar ba ilham ba tausayintane yakamashi dakamar yafasa aywatar da abin da yakawoshi dakin wata zuciyarce tacedama kayi abinda yakawoka kafita Dan ilham bakanwar lasabace in tatashi yimaka Nata kalar iskancin rami take kokarin turaka

ya gamsu da shawarar zuciyartashi danhaka Kai tsaye

yamikawa ilham invitations card din auransa Wanda yake acikin wata envelop

amsa tayi Tana jujjuyawa dago ido tayi Tana kallonsa danyayimata Karin bayani

cewa yayi bawani abubane aciki Illa katin bikina zan Kara aure Nanda wata guda mezuwa

jiri ilham tafara gani yayinda takwalla wata Kara tazube kasa sumammiya

hankalin anwar ne yatashi agigice yadagota yana kiran sunanta shuru bata amsaba firish yanufa yadauko ruwa ya yayyafamata

ajiyar zuciya tayi daga karshe tarushe da matsanancin kuka har yanzu Tana rungume ajikin anwar din  dagowa tayi Tana kallonshi ido cikin ido yayinda nata idon ke zubar da hawaye

[2/19, 18:15] Zahra muhd mahmud□: *ALLAH GATAN BAWA*□□□□□□□□□□

Zahra Muhammad mahmud

*DEDICATED TO ALLAH GATAN BAWA FANS, MORE ESPECIALLY, RUMAYSA, TA YAKASAI, MRS SHAMSUR, MMN ILLOUA,MAMAN BATULA,HASSANA AHMAD,UMMU TWINS,HAFSAT IDRIS,DASAURAN WAINDA BANKIRA SUNANSUBA THANKS YOU ALL*

*page 73-74*

Kallonshi ilham takeyi idonta nazubar dahawaye bakinta na rawa tace abban twins Allah yasanya alkhairi yasa abokiyar zamanka ce yabaku zuria dayyiba. Tana gama fadin haka tasake rushewa da kuka

Jikin anwarne yayi sanyi dajin adduar ilham tabbas yasan abinda yayimata da ciwo to amma yana ganin shine mafita

Cigaba tayi da kukanta Wanda anwar har zuciyarsa yakejinsa dasauri yatashi yafice daga dakin

Kifewa ilham tayi agurin Tana cigaba da kukanta

Biki se matsowa yakeyi dan yau saura sati guda kuma yaune ilham tatare asabon gidan anwar

Fadin kyau da haduwar gidan seya cinye data 1gb 😝bangama

Gidan samane danhaka ilham tazabi saman tana ganin zefiye mata duk da kasan yafi girma

Bangaren anwar ma asaman yake Wanda shi so yayi amaryarsa ta zauna asaman Amman bashida yadda zeyi ilham tazaba

Harda ameera da Mommyn Adnan suka rakota gidan dasu ihsan

Sata agaba mommy da ameera sukayi sunamata fada akan takwantar da hankalinta kishiya baakanta akafaraba kuma baakanta zaakareba

Sosai sukayimata fada gami da bata shawarwari

Daganan sukamata sallama suka tafi sabida gobe ne zaafara event na bukukuwan

Tunda ta tare agidan koso daya anwar bekwana agidanba danshi yace Seda amaryarsa zetare agidan

ilham ce kawai agidan se securities danko su twins suna gurin mommy abin bakaramin bata ran ilham yayiba Amman tabarwa Allah

Anyi event kalakala tun ana sauran kwana shida biki har zuwa yau da aka daura auren fadin irin mutanen dasuka halarci bikin bazeyiwuba Ammafa taro yay taro haka har aka gama shaida daurin auran anwar da amaryarsa nafeesat,adnan da amaryarsa ihsan,ameera da angonta moneer se fatan alkhairi kawai ga maauratan

Yaune kuma zaayi  dinner kuma ilham ma zata halarci gurin sabida duk Wanda akayi abaya batajeba se yaune zata wannan shawarar ameerace

Masu kwalliya ameera ta turamata gidanta akan su gyaramata auntinta da kyau

Kuma sunyi aykinsu yadda yakamata kamar yadda kuke ganin hotunan ilham da nafeesat a dp na group kunsan wainda suka gyara ilham sunyi ayki mekyau

Se wajen karfe Tara ilham tashirya ita da mukarrabanta acikinsu kuwa harda babbar aminiyarta wacce suka hadu a university suka karanci corse daya wato *sugura Abdullahi*sunyi shiga takece raini inda ilham takai kololuwa gurin haduwa suguran ma ba baya bace gurin haduwar haka suka Nufi motocin dake jiransu sukaisu dakin taron

Tuni amare da angwaye sun dadade dazuwa danhaka gurin acike yake

isarsu kofar hall din keda wuya tayakasai tahangosu dayace daga cikin kawayen ilham danhaka Kai tsaye gurin mc taje tace yasanar da isowar me girma uwargidan anwar hajiya ilham bukar shettima

Hakan ko akayi danshi mc harda kara gishiri danshi cewa yayi jamaa su saurara ga uwargida sarautar mata nan shigowa inda DJ yasaki wakar uwargida ran gida

wohoho sisters naso kunagurin kuga yadda ilham tashigo filin ga su twins agaba sune fulawa babies dinta yayinda itakuma suka jero da aminiyarta wato sugura

tafiya take cike da Jan aji da kasaita

anwar ne yamike zumbur dan tunda yake da ilham bata taba yimishi kyau irinnayauba dasauri yatako yazo har gabanta yana mata tafi gaba daya hall din aka dauki tafin murmushi suke yiwa juna naso da kauna

sugurace tayiwa ilham nuni data rungumeshi ayko dasaurinta tarungume anwar wayyo dadi haduwar jikinsu guri daya seda dukansu sukayi shock

Kiss anwar yayiwa ilham a goshi sannan yarike hannunta suka nufi gurin zama Dan tuni Ankara kujera agurin zamansa da amaryarsa nafeesa wacce se cika take Tana batsewa baitaba yan uwantama sunji haushin tarbar da anwar yayiwa ilham niko nace ayko  sede ku mutu danshine yafi cancanta daya tarbeta

zamansu kedawuya suka hada ido da ameera jinjina tamikomata yayinda ihsanma tamikomata murmushi tayimusu duka

haka taro yatashi kowa secewa yake mutumin dake da ilham mezeyi da nafeesa dangaskiya bakarya banbancin abayyane yake

koda suka isa gida su ameera se jinjinamata sukeyi hakade har aka kwashe amare zuwa gidajensu (amin afuwa banfadi a ina akayi taron bikinba to ameerade gidansu anwar suka dawo sabida hidimar bikin tayi sauki yayinda nafeesat ma gidan gwamnatin Kano dake Abuja suka dawo sabida bikin)

yankawo amarya sunkawota se habaici suke tayi itade ilham suna daki ita da kawayenta sugura taso ta tanka ilham ta hanata tace subarsu da halinsu

se sha daya nadare mijin sugura yazo yadauketa dama itace tarage kawai dansuma yan kawo amarya tuni sun watse

anwar ne yashigo gidan shikadai Dan wannan Karon yahana kowa rakoshi Kai tsaye sama yahaura dakin ilham yashiga inda yatarar da ita Tana karatun Qurani

